**COURSE GUIDE**

# HAU 107
# GABATARWA KAN NAZARIN AL'ADUN HAUSAWA (INTRODUCTION TO HAUSA CULTURAL STUDIES)

**Course Team** Dr. Ibrahim Abdullahi Sarkin Sudan (Course Writer) - UDUS
Professor Aliyu Muhammad Bunza (Course Editor ) - UDUS

**NATIONAL OPEN UNIVERSITY OF NIGERIA**

@ 2023 by NOUN Press
National Open University of Nigeria
Headquarters
University Village
Plot 91, Cadastral Zone
Nnamdi Azikiwe Expressway
Jabi, Abuja

Lagos Office
14/16 Ahmadu Bello Way
Victoria Island, Lagos

e-mail: centralinfo@nou.edu.ng
URL: www.nou.edu.ng

All rights reserved. No part of this book may be reproduced, in any form or by any means, without permission in writing from the publisher.

Published by:
National Open University of Nigeria

Printed 2023

ISBN:978-978-058-841-0

# HAU107: GABATARWA KAN NAZARIN AL'ADUN HAUSAWA

## Gabatarwa (Introduction)

Wannan kwas (HAU107), kamar sharer fage ne ga duk darussan da suke da alaƙa da al'adun Hausawa. Daga wannan darasi ne ake sa ran dalibai su san tushen duk wata al'ada ta Hausawa da yadda al'adun suke a yanzu. Darasin yana ɗauke da fasula masu ƙunshe da rukunai da kashe-kashe waɗanda suka fara da bayanin asalin kalmar al'ada daga kalmomi masu kinin ma'ana da ita. An yi bayanin ma'anar al'ada ta fuskoki da dama har ya zuwa ma'anar da ta yi daidai da ƙunshiyar wannan darasi, wato hanyar rayuwa da ta shafi wata al'umma. Haka kuma, an yi bayanin matakai da ake bi wurin gudanar da al'adu da yadda al'adu suke wanzuwa tsakanin Hausawa.

Baya ga haka, an kawo bayanin al'ada a tunanin Hausawa wanda ya shafi jindaɗi, da hanyoyin tattalin arziki, da siyasa, da addini. Daga wannan, an yi nazarin rabe-raben al'ada a tunanin Hausawa saɓanin yadda take wurin sauran al'ummu, da yadda al'ada take da ɗabi'a a tsarin zamantakewar Hausawa. An yi nazarin ɗabi'a inda aka bayyana kama da bambancinta da al'ada.

ƙarshen darasin ya kawo wasu tambayoyin auna fahimta da ake ganin in har ɗalibai suna iya amsa su, to lallai sun shirya wa jarabawa tun kafin ta zo. Akwai tushen bayani wanda zai yi jagorancin wurin da ɗalibai za su samu ƙarin bayani domin nazari cikin wasu ayyuka masu alaƙa da wannan kwas. An samar da wata kafa wadda ɗalibai za su yi amfani da ita domin tuntuɓar malamai saboda neman bayanan abin da suka shige musu duhu dangane da wannan kwas a kowane lokaci.

## Manufar Darasi (Course Aim)

Saboda a sami ingantaccen karatu da koyarwa, an fitar wa da kowane kashi manufa ta gaba ɗaya tun daga farkon darasi. Kawo wannan manufa daga farko za ta ba ɗalibai damar sanin inda kwas ɗin ya fuskanta tun farkonsa da abin da ake sa ran su gane cikinsa. Darasin ya ƙunshi darussa masu yawa, to amma muhimmai daga ciki su ne kamar haka:

- Sanin asalin kalmar al'ada da kalmomi masu kinin ma'ana da ita.
- Yadda Hausawa suke kallon al'ada a tunaninsu.
- Rabe-raben al'ada a tunanin Hausawa.
- [abi'un Hausawa kyawawa da munana.
- Yadda ɗabi'a ke rikiɗa zuwa al'ada.

## Yadda Za a Nazarci Kwas (Working Through the Course)

Darasin yana da tsari wanda zai ba ɗalibai damar yi wa kansu jagoranci cikin sauƙi ba tare da wata matsala ba. Hakan zai samu ne ganin an yi

wa kwas ɗin tsarin rukuni-rukuni mai ƙunshe da kashi-kashi da suke bi da bi. Kowane kashi yana da dangantaka da ɗan'uwansa bisa rabon da aka yi masu. Don haka, natsuwar ɗalibi zai taimaka wurin gane darasi tare da auna fahimta ta yin la'akari auna fahimta da jingar da ake gabatarwa a ƙarshen kowane darasi. Jingar da ke zuwa a duk ƙarshen kowane kashi, za ta taimaki ɗalibai yin hasashen irin tambayoyin da za a yi na jarabawa a ƙarshen kwas. Bin wannan mataki dama ce wadda idan an bi, ɗalibi yana iya dogaro da kansa ba tare da neman gudummuwar Malami ba. Kwas ɗin yana da lokaci na tsawon sati 15, wannan ya nuna cewa kowane kashi na kwas za a koyar da shi a kowane sati.
Yin nazarin kwas lokaci bayan lokaci dama ce wadda ba sai ɗalibi ya dinga kasancewa tare da malami ba a kowane lokaci. Ke nan bin kowane kashi mataki-mataki zai taimaka tare da amfani da jerin abubuwan da malami ya bayar domin yin jagoranci wurin samun ƙarin bayanai na faɗaɗa bincike da nazari.
A lokacin gabatar da wannan darasi, akwai abin da ya dace ɗalibai su mayar da hankali kansu.  Waɗannan abubuwa su ne:

1. Duk darasi ko kwas ya ƙunshi rukuni 3 ko 4.
2. Kowane rukuni yana da kashi 3 ko 4.
3. Kowane kasha yana da sashen auna fahimta.
4. Kowane darasi yana da jingar da za a yi a gida.
5. Kowane darasi ko kwas akwai manazarta da wasu wuraren da ake iya yin ƙarin  nazari.

**Kashe-kashen Kwas (Study Units)**
An raba wannan kwas zuwa rukuni huɗu, kowane rukuni yana ƙunshe da kashi huɗu in ban da rukuni na huɗu wanda kashi biyu ne rak. Kowane rukuni yana matsayin darasin da za a gudanar a sati (mako) guda. Ke nan ana da darussan sati 14 kafin kwas ɗin ya kamala. An yi tambayoyin auna fahimta a ƙarshen kowane kashi, waɗannan tambayoyi idan ɗalibai suka nazarce su; tare da yin jingar da ke biye, darasin zai yi taushi ƙwarai ga ɗalibai.

A ƙoƙarin ganin ɗalibai sun fahimta tare da samun cikakken bayani, an kawo manazarta domin ta taimaka wurin samun bayanai game da darussan da aka gabatar. Neman su tun wuri zai taimaka, ba sai lokaci ya ƙure an nema a rasa ba. Littafn Bunza (2006) da na Funtua da Gusau (2010) ya kyautu a neme su. Sauran litatafai masu bayanin al'adun Hausawa waɗanda ba a ambace su ba, su ma za su taimaka ƙwarai in an same su.

**Auna Fahimta (Assignment)**
Fasalin wannan kwas ya nuna cewa ɗalibi ba sai ya ga malami a zahiri ba, don haka ne aka samar da hanyoyi uku na jaraba fahimtar ɗalibi. Hanyar farko ita ce wadda ake kawo tambayoyin auna fahimta a ƙarshen kowane darasi, daga bisani a bayar da jingar da ɗalibai za su yi a

ƙarshen darasi; daga ƙarshe kuma a gabatar da jarabawar ƙarshen zangon karatu mai nuni da darasi ya ƙare.

Zubin auna fahimtar da ake yi a duk ƙarshen darasi, tamkar wata jarabawa ce ƙarama; to sai dai tana ɗauke da maki 30 daga cikin kaso 100. Wannan ya nuna idan dalibai ya amsa tambayoyi 2 cikin uku, kowace tambaya tana da maki 15. Ragowar maki 70 su ne za a samu daga jarabawar ƙarshen kwas ɗin.

Bisa tsarin wannan karatu, ana yin jarabawa ne daga gida, amma ba a cikin ajin darasi ba. Ana yin jarabawar ta hanyar intanet. Hakan ya nuna tilascin sani da naƙaltar na'ura mai ƙwaƙwalwa abu ne da ya zama wajibi baya ga muhimmancinsa ga ɗalibai.

**Jinga (Tutor Marked Assignment)**
Jingar da ake bai wa ɗalibai wani shiri ne da zai kimtsa ɗalibai tun kafin zuwan jarabawa. ƙoƙarin iya amsa jingar kowane kashi na darasi dama ce ga ɗalibai su fara naƙaltar yadda za ta kasance a ƙarshen zangon karatu. [aliban da suka yi azama wurin yin ƙoƙarin amsa jinga, sun sauƙaƙa wa kansu fuskantar amsa tambayoyin jarabawa wadda za a yi a ƙarshen darasi

**Jarabawar ƙarshen Darasi (End of Course Examination)**
Jarabawar ƙarshe hanya ce wadda ake yin awon fahimtar ɗalibai dangane da abin da aka koyar da su. Ta wannan hanya ake fahimtar ko sun gane darasin, ko kuwa wani ɓangare kaɗai ya gane. Jarabawar takan kasance ta ɗauki kaso 70 cikin kashi 100 na kwas. Wannan fasali abin da dalibai ba su gane ba game da shi, ana samo tambayoyin ne daga cikin tambayoyin auna fahimta ko jinga. Bisa wannan dalili ake ganin cewa duk wanda ya yi ƙoƙarin naƙalta tare da iya amsa waɗancan tambayyoyi, lokacin da jarabawa ta zo; zai tunkare ta ba tare da fargaba ba.

**MAIN COURSE**

## CONTENTS

**Ga fuskar yadda darasin zai kasance**

**RUKUNI Na 1 MECE CE AL'ADA?.......................... 1**

Kashi Na 1 Kalmar Al'ada………………………… 1
Kashi Na 2 Al'ada da Kalmomi Masu Kinin Ma'ana 7
Kashi Na 3 Matakan Gudanar da Al'ada…………… 13
Kashi Na 4 Matakan Wanzar da Al'ada…………… 18

**RUKUNI NA 2 AL'ADA A TUNANIN HAUSAWA.. 23**

Kashi Na 1 Jin Daɗi……………………………….. 23
Kashi Na 2 Tattalin Arziƙi………………………… 28
Kashi Na 3 Addini………………………………… 33
Kashi Na 4 Shugabanci…………………………… 39

**RUKUNI NA UKU RABE-RABEN AL'ADA A IDON HAUSAWA………………… 43**

Kashi Na 1 Al'adun Gargajiya Zalla…………….. 43
Kashi Na 2 Al'adun Fasahar Hannu (Material Culture)…………………… 50
Kasha Na 3 Al'adun Fasahar Baka………………. 55
Kashi Na 4 Cuɗaɗɗun Al'adu…………………… 60

**Ga fuskar yadda darasin zai kasance**

**Rukuni na 1 CE AL'ADA?**


Kashi Na 1 Kalmar Al'ada.
Kashi Na 2 Al'ada da Kalmomi Masu Kinin Ma'ana
Kashi Na 3 Matakan Gudanar da Al'ada.
Kashi Na 4 Matakan Wanzar da Al'ada


## KASHI NA 1 KALMAR AL'ADA

**Abubuwan da ke Ciki**

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufofin Darasi
1.3 Asalin Kalmar Al'ada
 1.3.1 Fashin Baƙin Kalmar Al'ada
 1.3.2 Muhimmancin Al'ada
 1.3.3 Hanyoyin Tantance Al'adun Hausawa Auna Fahimta
 Auna fahimta
1.4 Taƙaitawa
1.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
1.6 Manazarta
1.7 Amsoshin Auna Fahimta



### 1.1 Gabatarwa

Matakin farko a wannan darasi shi ne ɗalibi ya san abin da ake nufi da al'ada. Sanin asali da ma'anar kalmar cikin luggar Larabci da kuma Hausa zai taimaki ɗalibi ya san inda kwas ɗin zai sa gaba. Wannan kwas zai yi ƙoƙarin fayyace me ake kira al'ada a fagen nazari, da abubuwan da al'adun Hausawa suka ƙunsa. Sanin al'ada da rabe-rabenta su ne ginshiƙi wurin mai neman sanin al'adun Hausawa. Haka zai bayar da damar sanin ainihin al'adun Hausawa da waɗanda ba nasu ba da irin kutse ko tasirin da zamani ya yi cikin al'adun Hausa.

## 1.2 Manufofin Bincike

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- Bayanin asalin kalmar al'ada.
- Yin bayanin kalmar al'ada a Larabci da yadda ma'anar take a Hausa.
- Iya yi wa kalmar al'ada fashin baƙi domin ta dace da muhallin da ta fito cikin zance.

## 1.3 Asalin Kalmar Al'ada

Kalmar Al'ada asalinta Balarabiyar kalma ce wadda Hausawa suka aro daga Larabci zuwa Hausa. Ahmed da Daura (1970: 9-11) sun yi bayanin cewa akwai kalmomin Hausa waɗanda asalinsu daga harshen Larabci suke. A cewarsu, dangantakar Hausawa da Larabawa ta daɗe tun lokacin cinikayya tsakanin ƙasashen Afirka da Larabawa. Sun ƙara da cewa, kalmomin Hausa irin su: ''Al'ada'' da waɗanda suka fara da 'Al' tushensu na asali shi ne harshen Larabci. Idan kuwa haka ne, kalmar al'ada ararriyar kalma ce wadda a yau ta narke cikin harshen Hausa. To sai dai, ba za a rasa kalmar Hausa ta asali mai ƙunshe da irin wannan ma'ana a Hausa ba.

### 1.3.1 Fashin Baƙin Kalmar Al'ada:

Kalmar al'ada tana ɗaukar ma'anoni iri-iri gwargwadon muhallin da aka yi amfani da ita. ƙamusun Bargery (1934: 16) ya bayyana al'ada da ta'ada ko ɗabi'a ko tada ko tsabi'ia wadda ke nufin haila ko fashin Sallah ko wanki ko bin wata. Ma'anar da Bargery ya bayar ta fi karkata ne ga fitar mataccen jini na ƙa'ida wanda mata ke yi duk wata. Wannan al'ada ta keɓanta ne ga mata zalla, banda maza.

[angambo (1984: 38) ya bayyana al'ada da cewa: "Al'ada ita ce abar da aka saba yi, yau da gobe. Al'ada wani yanki ne na rayuwa da ta ƙunshi halaye da ɗabi'u da aka saba yi, yau da gobe da kullum don rayuwa".

Bunza (2006: xxxii) ya ce al'ada tana nufin dukkanin rayuwa ɗan Adam tun daga haihuwarsa har ya zuwa kabarinsa. Babu wata al'umma da za ta rayu a doron ƙasa face tana da al'adar da take bi, kuma da ita ake iya rarrabe ta da wata da ba ita ba.

Sa'id da wasu (2006: 9) sun bayyana ma'anar al'ada da cewa hanyar rayuwa al'umma, ko jinin haila ko wani irin hali daban na mutum ko magani ko tsafi. Ma'anarsa ta farko ita ce ke da kusanci da wannan kwas

domin ana ƙoƙarin sanin yadda hanyar rayuwar Hausawa (al'adarsu) take ne.

Gusau (2010:2) ya ce al'ada ita ce tafarki wanda wata al'umma take rayuwa a cikinsa dangane da yanayin abinci da tufafi da muhalli da rayuwar aure da haihuwa da mutuwa da wasu hulɗoɗin rayuwa kamar maƙwabtaka da sana'o'i da kasuwanci da shugabanci da bukukuwa da sauran abubuwa waɗanda suke da alaƙa da haka. Ita wannan ma'ana ta fayyace abubuwan da al'umma suke yi ne waɗanda su ne al'ada a tsarin rayuwar Hausawa. Ta yiwu abin da aka lissafo a matsayin al'ada ga Hausawa, ya zama ba ya cikin abin da wata al'ummar take ɗauka a matsayin al'ada.

Ta yin la'akari da waɗannan ma'anoni da suka gabata, al'ada ita ce hanyar rayuwa wadda wata al'umma ta gada tun iyaye da kakanni a matsayin matakai da ake gudanar da rayuwa. Irin wannan hanya tana iya bunƙasa a wani lokaci ko kuma ta tsufa ta mutu ko masu ita su watsar su rungumi wani abu sabo a matsayin al'ada. Wannan ya nuna cewa, al'ada tana iya sauyawa daga lokaci zuwa lokaci gwargwadon ci gaba ko hulɗa da wata al'ummar.

## 1.3.2 Muhimmancin Al'ada

Al'ada abu ce mai matuƙar muhimmanci a rayuwar Hausawa. Ita ke yi wa mutum jagoranci wurin sanin matsayinsa cikin al'umma, da irin hurumin da yake iya shiga da wanda ba nasa ba ne. Wani amfani na al'ada shi ne, tana kawo haɗin kai a tsakanin masu gudanar da ita. Dalili shi ne, a wasu lokuta ana taruwa ne domin gudanar d al'ada cikin gida ko zuriya ko al'umma guda. Wannan ya kawo son juna da taimakekeniya ganin cewa hanyar tafiyar da rayuwarsu ɗaya ce, ko da kuwa ba gida guda aka fito ba. A duk wurin da aka haɗu, ana zumunci da kare mutuncin juna. Nwankpa (2006: 154) ya ce al'ada tana taimakawa wurin wanzuwar al'umma daga wannan zango zuwa wancan. Ya ce da zarar babu al'ada a tsakanin al'umma, to akan mance da su tamkar sun ɓace. Wannan bayani ya jadda muhimmancin al'ada a tsakanin kowace irin al'umma.

## 1.3.3 Hanyoyin Tantance Al'adun Hausawa

Wannan yana Magana ne kan irin hanyoyin da ake iya gane Hausawa saboda cewa al'ada ita ce hanyar rayuwa. To ta yaya ko waɗanne hanyoyi na gudanar da rayuwa ake iya gane Hausawa? Akwai hanyoyi da dama da ake iya gani a gane cewa wannan Bahaushe ne ta la'akari da yadda yake ko yake tafiyar da rayuwarsa.

Ana gane Hausawa ta hanyar tsagarsu ta gargajiya wadda ke iya bambanta ko a cikin Hausawan. Katsinawa da Gobirawa da Kanawa da Zamfarawa duk yanayin tsagarsu ta bambanta da juna. Misali, Kanawa suna da 'yarbaka guda uku-uku, su kuwa Katsinawa suna da zane dogaye caɓa-caɓa a kumatun hagu da dama, sannan tsagar gado biyu ce. Safana (2010) ya ce tsaga tana iya nuna asali da sana'a. Zamfarawa kuma tsagarsu ta yi kusan kama da ta Katsinawa to sai dai sun bambanta bisa tsarinsu.

Wata hanya da za a iya gane al'adun Hausawa ita ce ta hanyar sunayensu. Al'adun Hausawa sun samar da hanyoyi masu yawa da ake bi wurin sanya wa abin da aka haifa suna. Ana amfani da sifar jiki, ko lokacin haihuwa ko yanayin haihuwa ko wani hali da Uba ko gida yake ciki a sanya suna ga abin da aka haifa. Hakan shi ya samar da sunaye irin su: Talle da Audi da Cindo da Jadi da Mijinyawa da Korau da dai sauransu.

Abinci wata hanyar rayuwa ce da take bambanta daga wannan al'umma zuwa waccan. Duk da yake cewa ana iya samun bambance-bambance na nau'in abinci tsakanin Hausawa mazauna Zariya da waɗanda ke zaune Kano da Katsina ko Zamfara, Hakan bai hana su zama Hausawa ba; amma dai yanayin muhalli da tsarin rayuwa ya sa nau'in abincinsu ya bambanta da junansu. Waɗannan bayanai game da al'ada a rayuwar Hausawa, sun nuna cewa akwai bambanci na al'adu tsakanin Hausawan ƙasar Hausa. Babban abin da ya kawo bambanci a tsakaninsu shi ne, saɓanin yanayin wurin zama wanda shi ke ba da damar yadda za a gudanar da rayuwa. Nisa tsakanin waɗannan Hausawa da waɗancan ba zai ba su damar yin rayuwa iri guda ba, sai dai a ce ƙunshiyar yadda ake tafiyar da rayuwar guda ce.

Auna Fahimta

| | |
|---|---|
| 1- | Me ya sa aka ce kalmar al'ada daga Larabci take? |
| 2- | Ma'anoni nawa za a iya hange cikin kalmar al'ada? |



## 1.4 Taƙaitawa

Wannan darasi, an yi ƙoƙarin bin sawun asali da ma'anonin kalmar al'ada a Hausa, da yadda take da muhimmanci da hanyoyin gane al'adar Hausawa.

## 1.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi

Al'ada: - wani yanki ne na rayuwa da ta ƙunshi halaye da ɗabi'u da aka saba yi, yau da gobe da kullum don rayuwa.

## 1.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

Bargery, G. P. (1934). *A Hausa–English Dictinary.* London: Oxford University press.

Bunza, A. M. (2006). *Gadon Feɗe Al'ada.* Lagos: Tiwal Nigeria Limited.

Ɗangambo, A. (1987). *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa.* Kano: Triumph.

Funtua, A. I. da Gusau, S. M. (ed) (2010). *Al'adu da Dabi'un Hausawa da Fulani.* Kaduna: El-Abbas printers & Media Concept.

Sa'id, B. da wasu (ed) (2006). *Ƙamusun Hausa na Jami'ar Bayero.* Zaria: Ahmadu Bello University press Ltd.

## 1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1- Me ya sa aka ce kalmar al'ada daga Larabci take?
Saboda an aro kalma ne daga Larabci

2- Ta wace hanya za a iya gane al'adun Hausawa?
i-Ana gane Hausawa ta hanyar tsagarsu ta gargajiya wadda ke iya bambanta ko a cikin Hausawan. Katsinawa da Gobirawa da Kanawa da Zamfarawa duk yanayin tsagarsu ta bambanta da juna. Misali, Kanawa suna da 'yarbaka guda uku-uku, su kuwa Katsinawa suna da zane dogaye caɓa-caɓa a kumatun hagu da dama, sannan tsagar gado biyu ce.

ii-Wata hanya da za a iya gane al'adun Hausawa ita ce ta hanyar sunayensu. Al'adun Hausawa sun samar da hanyoyi masu yawa da ake bi wurin sanya wa abin da aka haifa suna. Ana amfani da sifar jiki, ko lokacin haihuwa ko yanayin haihuwa ko wani hali da Uba ko gida yake ciki a sanya suna ga abin da aka haifa. Hakan shi ya samar da sunaye irin su: Talle da Audi da Cindo da Jadi da Mijinyawa da Korau da dai sauransu.

iii-Abinci wata hanyar rayuwa ce da take bambanta daga wannan al'umma zuwa waccan. Duk da yake cewa ana iya samun bambance-bambance na nau'in abinci tsakanin Hausawa mazauna Zariya da waɗanda ke zaune Kano da Katsina ko Zamfara, Hakan bai hana su zama Hausawa ba; amma dai yanayin muhalli da tsarin rayuwa ya sa nau'in abincinsu ya bambanta da junansu. Waɗannan bayanai game da al'ada a rayuwar Hausawa, sun nuna cewa akwai bambanci na al'adu tsakanin Hausawan ƙasar Hausa.

**KASHI NA BIYU AL'ADA DA KALMOMI MASU KININ MA'ANA**

## Abubuwan da ke ciki

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufofin Darasi
2.3 Al'ada da kalmomi masu kinin ma'ana
  2.3.1 Ɗabi'a
  2.3.2 Gado
  2.3.3 Gargajiya
  2.3.4 Sabo
  2.3.5 Tada
  Auna Fahimta
2.4 Taƙaitawa
2.5 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi
2.6 Manazarta
2.7 Amsoshin Auna Fahimta



## 2.1 Gabatarwa

Wannan fasali zai yi bayani ne game da wasu kalmomi na Hausa bisa asalinsu waɗanda suke ɗauke da ma'anoni masu kusanci da al'ada a fannin nazarin al'adun Hausawa. Fasalin gabata shimfiɗa ce da ke nuna yadda kalmar Larabci maye ta asali, to amma yanzu ne za a ga kalmomin da ake amfani da su a maimakon al'ada tun asali.



## 2.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

i. Yin bayanin kalmomi masu kinin ma'ana da al'ada.
ii. Kawo misalai daga zantukan hikima game da kalmomi masu kinin ma'ana da
al'ada.
iii. Fayyace yadda bayanin kowace kalma ke iya zama al'ada.

## 2.3 Al'ada da kalmomi masu kinin ma'ana

### 2.3.1 Ɗabi'a

Sa'id da wasu (2006:116) sun bayyana ma'anar ɗabi'a da cewa halin mutum ko al'adarsa. Ma'anar tasu ta kawo abin da ɗabi'a ta ƙunsa. Halin mutum shi kaɗai ake kira ɗabi'a. Ita kuwa al'ada tana iya zama ta mutane da yawa.

Gusau (2010: 2) cewa ya yi ɗabi'a halaye ne waɗanda mutane suke yi ɗaya-ɗayansu kuma aka fahinci kowane mutum da irin hali nasa na daban da wani. A nan ma halin da wani yake aikatawa iya rikiɗewa ya zuwa al'ada a duk lokacin da aka ɗauki halin wani a matsayin hanyar rayuwa. Hausawa sauna cewa: "Halin Uwa [a ke ɗauka''. Wannan ya nuna cewa abin da '[a' ya ga Uwa tana yi, zai gudanar a matsayin al'ada saboda ya ga Uwa tana yi; tunaninsa shi ne abin ƙwarai ne.

Bunza (2006: xxvi) yana cewa hali a cikin jini yake, har abada ba a raba mai shi da shi. Ana samun zantukan hikima masu bayanin hali kamar haka:

Hali zanen dutse.
Hali abokin tafiya.
Mai hali, ba ya barin halinsa.

Waɗannan misalai, sun nuna cewa hali wani abu ne da yake cikin jini wanda ake iya gado daga iyaye da kakanni. In kuwa haka ne, ke nan ɗabi'a a matsayin hali tana iya zama al'ada idan aka ɗauki lokaci mai tsawo.

### 2.3.2 Gado

Sa'id da wasu (2006: 149) sun bayyana gado da cewa muƙami ko hali ko sifa ko kaya da mutum ya gada. A nan hali da abin da mutum ya gada ta fuskar yanayin yadda ake aiwatar da rayuwa, su ne bayanan gado masu kusanci da al'ada.

Halin da aka gada wurin iyaye kuma aka tarar ana aiwatarwa, ya zama gado kuma al'ada, a cewar Bunza (2006: xxvi). Zantukan hikima na Hausawa sun fito da gado fili kamar haka:

Gado ba ya wofinta.
Kunya aka tsoro, mutuwa ta zama gado.

A bar Agola ya sha kunu, rabon gado ba nasaba.

Ke nan, waɗannan zantukan hikima sun tabbatar da gado abu ne da aka tarar wurin iyaye da kakanni ana yi. Don haka, aiwatar da wani abu wanda magabata suke yi gado ne, gado kuma ya koma al'ada.

### 2.3.3 Gargajiya

Sa'ida da Wasu (2006:159) sun bayyana gargajiya da ɗabi'a ko wani kaya irin na zamanin da. Bunza (2006: xxvi) yana cewa, gargajiya ta samu ne daga gadajjen abu wanda Bahaushe ke yi musamman abin da ya saɓa da aƙidojin Musulunci. A faɗaɗe, gargajiya ta shafi tsarin rayuwa wadda aka gada tun ga iyaye da kakanni a ɓangaren abinci ko sutura ko muhalli ko harshe ko magani da duk wata hanyar rayuwa wadda ba ta shafi wayewar zamani ba.

A ɓangaren gargajiya, duk wani abu da aka san cewa Hausawa sun gaji abin wurin iyaye da kakanni da zaran wani ya aiwatar da wannan abu; sai a ce an yi gargajiya. Misali, duk wanda aka ga yana cin abinci kamar Rama ko Zogale ko Dankali ko Rogo, akan ce da shi yana cin abincin gargajiya. Dalilin cewa haka shi, nau'in abinci ne na Hausawa wanda suke nomawa kuma sun gaje shi a matsayi cimaka wurin iyaye da kakanni ba tare da tasirin zamani a ciki ba.

A cikin zamantakewa yau da kullum tsakanin Hausawa, waɗanda suke rayuwa irin ta Maguzanci ana ganinsu a matsayin 'yan gargajiya saboda suna gudanar da tsarin rayuwa irin ta gargajiya; wadda suka gani suka gada tun iyaye da kakanni. Bahaushen Musulmi idan aka lura cewa yana yin bori ko tsafi ko wasu halaye da suka yi saɓani da koyarwar Musulunci, akan kira shi da ɗan gargajiya.

Tsarin rayuwar Hausawa a yau cikin lamuran aure da haihuwa, akan ware wasu al'adu da za a gudanar a matsayin al'adun gargajiya. Ana ratsa al'adun cikin bukin domin tabbatar da cewa sun gaji gargajiya ko da kuwa za a aiwatar da zamananci daga bisani. Misali, a lokacin bukin aure a yanzu, ana ware ranar ƙaryawa da nufin nuna al'adun Hausawa na gargajiya a ɓangaren sutura da abinci da kiɗa da rawa da waƙe-waƙe.

Al'adun da ke cikin bukin haihuwa kamar yin barka ko ƙauri bayan wasu kwanaki da yin haihuwa kafin suna, gargajiya ce da aka gada wurin iyaye da kakanni. Haka kuma, gudanar da taron raɗa suna wanda maza kan yi a ran bakwai da haihuwa, taro ne na gargajiya wanda zuwan addinin Musulumci ya sa Hausawa suka yi masa kwaskwarima. Waɗannan misalai sun nuna cewa ga yadda wasu al'adu suke waɗanda ake gudanar da su a matsayin gargajiya cikin rayuwar Hausawa. Ko da yake, da yawan wasu al'adun gargajiya a yanzu sun tasirantu da zamani.

### 2.3.4 Sabo

Sabon yana nufin abin da mutum ya saba yi a duk wani lokaci cikin rayuwarsa musamman yin abin da ya tarar iyaye da kakanni suna yi. Sabo yana iya zama yin abu wanda yanayin wurin zama ko al'umma ta saba da shi a matsayin hanyar tafiyar da rayuwa. Bunza (2006: xxvi) ya ce sabo shi ne abin da aka saba da shi yau da gobe kamar al'ada. Ke nan sabo wani abu ne da yake iya shiga jinin mai yin abu har ya zama an gaje shi.

Zantukan Hausawa na hikima rumbu ne da ke ƙunshe da bayanai masu nuna al'adu. Sabo ya bayyana cikin wasu karin maganganu domin tabbatar da shi a matsayin al'ada. Misali,

Sabo turken wawa.
Sabo jini ne ba ya sauyawa.
Hannu ya iya jiki ya saba.
Sabo da maza jari.

Waɗannan misalai suna bayyana yadda sabo ya zama al'ada a duk wurin da ake aiwatar da rayuwa. Abin da aka saba yana zama jiki ga mai yi ta yadda 'ya'ya da jikoki za su ɗauke shi a matsayin abin da suka tarar iyaye da kakanni suka saba aiwatarwa.

### 2.3.5 Tada

Tada ita ce tilasta wa rayuwa barin aikata wani abu ko barin yin aiki ko amfani da wani abu ko zuwa wani wuri domin wani dalili na musamman da mai wannan tadar ya kiyaye. Wanda yake aiwatar da tada ya ba da gaskiya cewa, aikata saɓanin abin da tada ta ajiye; yana tattare da sakamako na musamman da ya shafi rashin lafiya ko halaka. Irin wannan dalili ya sa idan mutum ya san cewa wani abu tada ce a gareshi; yake kiyayewa saboda gudun karya doka ko ƙa'idar da aka gindaya game da ita.

Bunza (2006: 80) ya nuna cewa tada ta ratsa kusan kowane ɓangare na rayuwar Hausawa. Wannan ya sa tada ta kasance wani ɓangare na al'adun Hausawa kuma kalma mai iya yin kafaɗa da kafaɗa da al'ada a fagen nazari. Rabe-Raben tada wanda Bunza (2006) ya bayyana, sun rabu zuwa gida goma sha uku kamar haka:

a. Tadar kan gida.
b. Tadar Iskoki ga dokinsu.
c. Tadar mafari ko sanadi.
d. Tadar cutukan jini.
e. Tadar magani.
f. Tadar kai.
g. Tadar yanayi ko lokaci.

h. Tadar ado.
i. Tadar sana'a.
j. Tadar tsoron dangi ko zuriya.
k. Tadar tsare lafiyar jiki.
l. Tadar Alfarma.
m. Tadar kunya.

A tsarin rayuwar Hausawa, ba lallai ne waɗannan su zama su kaɗai ne ire-ire tadojin da Hausawa suke da su ba kamar yadda Bunza (2006) ya ce. Ke nan, ana iya samun wasu tadojin da suka shafi yadda ake tafiyar da rayuwa ta hanyar cusa wa kai wata aƙida ta tilasta wa kai horo domin samun yardar Iskoki. Bijire wa wannan horo ko saɓa wa ƙa'idar kuma yakan kasance tattare da sakamako na rashin jin daɗi.

Misalin tada a rayuwar Hausawa shi ne, a sami wani gida ko zuriya da ta tilasta wa kanta barin cin wata dabba. Misali, barin cin Damo saboda gudun ɗaukar hali irin na Damo. Haka kuma, idan wani ya ci wani abu ya mutu, to mutanen wannan gida ko zuriya za su mayar da wannan abu tada saboda gudun sake faruwar abin da ya auku ga wani magabaci a baya.

Auna Fahimta

1. Mece ce gargajiya?
2. Ta yaya gado ke iya zama gargajiya.

## 2.4 Taƙaitawa

Wannan darasi ya yi bitar kalmomi masu kusancin ma'ana da kalmar al'ada domin a ji dalilin kasancewar su al'ada. To sai dai kowane ɗaya daga cikinsu ba zai ɗauki dunƙulalliyar ma'ana ta al'ada ba, musaya kalmar da wata baƙuwar kalma domin ta ƙunshi dukkan hanyoyin rayuwa.

## 2.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi

Gargajiya: - wani hali ne irin na zamanin da

## 2.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

Bargery, G. P. (1934). *A Hausa–English Dictinary.* London: Oxford University press.

Bunza, A. M. (2006). *Gadon Feɗe Al'ada.* Lagos: Tiwal Nigeria Limited.

Ɗangambo, A. (1987). *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa.* Kano: Triumph.

Funtua, A. I. da Gusau, S. M. (ed) (2010). *Al'adu da Dabi'un Hausawa da Fulani.*
Kaduna: El-Abbas printers & Media Concept.

Sa'id, B. da wasu (ed) (2006). *Ƙamusun Hausa na Jami'ar Bayero*. Zaria: Ahmadu Bello University press Ltd.

## 2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1- Mece ce gargajiya?

Gargajiya da ɗabi'a ko wani kaya irin na zamanin da. Haka ma, gargajiya ta samu ne daga gadajjen abu wanda Bahaushe ke yi musamman abin da ya saɓa da aƙidojin Musulunci. A faɗaɗe, gargajiya ta shafi tsarin rayuwa wadda aka gada tun ga iyaye da kakanni a ɓangaren abinci ko sutura ko muhalli ko harshe ko magani da duk wata hanyar rayuwa wadda ba ta shafi wayewar zamani ba.

2- Ta yaya gado ke iya zama gargajiya

Gado kan iya zama gargajiya saboda gargajiya ta shafi wani hali da iyaye da kakanni suke gudanarwa tun lokaci mai tsawo, shi kuma gado a gaji wani wani abu da iyaye suke aiwatarwa tun lokaci mai tsawo. Bisa wannan muke ganin cewa gado yakan iya zama gargajiya

# KASHI NA UKU MATAKAN GUDANAR DA AL'ADA

## Abubuwan Da Suke Ciki

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufofin Darasi
3.3 Matakan gudanar da al'ada
 3.3.1 Matakin Mutum
 3.3.2 Matakin Gida
 3.3.3 Matakin Gari
 3.3.4 Matakin ƙasa
 3.3.5 Matakin Duniya.
 Auna Fahimta
3.4 Taƙaitawa
3.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi
3.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



## 3.1 Gabatarwa

Al'da ana gudanar da ita ne a cikin matakai daban-daban har zuwa lokacin da za a ce ta zama al'adar da ta yi fice a duniya. Wannan ɓangare zai kalli matakan da ake aiwatar da al'ada ne tun faruwarta har ya zuwa bazuwarta cikin al'umma.



## 3.2 Manufofin Darasi

- A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci: Yadda ake samun al'ada.
- Yadda al'ada ke zama al'adar gari ko gida.
- Fayyace al'adun gida daban da al'adun gari ko al'umma.



## 3.3 Matakan gudanar da al'ada

### 3.3.1 Matakin Mutum

Mafarin samuwa da gudanar da al'ada wadda za ta zama silar gudanar da hanyar rayuwa shi ne inda wani mutum ya fara aiwatar da wani abu shi kaɗai. Ba abin mamaki ba ne mutum guda ya fara aiwatar da rayuwa

shi kaɗai. Bisa tsarin zamantakewa irin ta Hausawa, akwai Tunga da ƙaura da Runji inda wani ko wasu za su tashi daga bagirensu zuwa wani, ko kuma su matsa daga wannan bagire zuwa gefensa can su kaɗai bisa wasu dalilai na buwaya ko aikata wani laifi cikin al'uma. A irin haka, rayuwarsu takan fita daban da ta sauran mutane. Daga lokacin da wannan mutum ya fara zuriya, to lallai za su gudanar da rayuwa irin wadda suka ga yana yi. Wannan rayuwa da za su yi ta bambanta da ta sauran jama'ar da suke maƙwabtaka da su, saboda wanda ya fara irin wannan rayuwa da suka gada ya fara ta ne tun yana zaman kaɗaici.

### 3.3.2 Matakin Gida

Duk gidan da ya tsiro daga tsatson Tungar wani ko Runji ko ƙaura, to lallai za a ga yanayin rayuwarsu ta bambanta da ta sauran mutane. Haka kuma, tsarin zamantakewar Hausawa na gargajiya ya nuna cewa kowane gida suna da irin sana'ar da suke aiwatarwa a matsayin abin da suka gada wurin iyaye da kakanni. Su kuwa sana'o'in gargajiya waɗanda aka gada a matakin sana'ar gida, tattare take da al'adu da suka keɓanta da su. Ita kanta sana'a farko ta kasance al'ada kuma gado a wurin duk ahalin wannan gida. Kowane yaro ya san yadda ake aiwatar da sana'ar gidansu da horo da hani da suka shafe ta, da nau'in magani da ake sha ko ake bayarwa ga wasu wanda ya danganci wannan sana'a. Daga samuwar haka, sai gida ya faɗaɗa ta yadda ko wasu sun yi nasu gida, suna riƙe da al'adar zuriyarsu ko gidansu da suka gada tun iyaye da kakanni. Ana samun irin wannan al'ada wurin manoma da maƙera da masunta da masaƙa da sauransu.

### 3.3.3 Matakin Gari

Gari yana ya zama cikin fasalin al'umma ɗaya a matakin farko kafin zuwan baƙi daga wasu wurare. Galibi garuruwa da ƙauyuka da karkara tushensu guda ne har ya zuwa lokacin da za su bunƙasa, wasu jama'ar su yo ƙaura zuwa wannan gari da zama na har abada. Al'ada tana iya zama ta gari duka bisa la'akari da wurin zama tare da yanayin muhalli ko tushensu bisa zuriya. Wannan zai samar da al'ada wadda kowa ke bi a dukkannin ɓangarorin rayuwarsu. Misali, galibin mutanen Arugungu masunta ne. Sun gaji sana'ar Su da iya ruwa. Don haka, mutanen garin suna da al'ada ta bai ɗaya, kafin daga bisani su haɗu da mutanen da ba Argungawa ba masu al'ada ta daban da tasu. A dubi mutanen Zariya waɗanda ake kira Zage-zagi, fitaccen abincinsu na gargajiya shi ne Fate. Su kuwa Zamfarawa sun gaji abinci mai suna Hoce. Ke nan al'adu suna samuwa a matakai daban-daban har da na gari kafin a ji bullarsu a wasu sassa na ƙasa ko duniya.

### 3.3.4 Matakin ƙasa

Al’adar ɗaiɗaikun mutane a cikin wata al’umma idan ta ginu, masu yin ta suka yawaita har suka zama gari mai zaman kansa; suna iya zama daban da sauran mutane. Hakan zai sa a san da su a duk faɗin ƙasar da suke ta yadda idan an ga mai tafiyar da rayuwa cikin wani tsari, an san wurin da ya fito. Misali, a ƙasar Hausa an yarda cewa duk Bakanon asali ɗan kasuwa ne, ya iya kasuwanci ko wata sana’a da zai samu rufin asiri. An aminta cewa Katsinawa da Zamfarawa manoma ne bisa al’ada, amma sukan yi wasu sana’o’i baya ga noma idan kaka ta yi. Ke nan, a duk wurin da za a haɗu cikin ƙasar domin yin wani taro, kowa ƙoƙarinsa shi ne ya nuna hanyar rayuwarsa da ya gada iyaye da kakanni wadda ya iya. Al’adar da aka tabbatar da ita ce fitacciya ga kowace al’umma, tana iya zama al’adar da ke iya wakiltar ƙasa a lokacin wani taron buki na ƙasa ko duniya. Misali, ƙasar Hausa a jumlace al’adarsu ta fuskar tattalin arziƙi ita ce sana’ar noma, sai kasuwanci. Kowane yanki na ƙasar da irin abin da suke nomawa wanda ya yi daidai da yadda yanayin ƙasar wurin take. Wannan shi ne tushen bambance-bambance ta fuskar al’adu a ɓangaren abinci da sutura da tsarin muhalli, da kasuwanci.

### 3.3.5 Matakin Duniya

Al’adar da mafi yawancin mutanen ƙasa suke yi a matsayin hanyar rayuwar da suka saba da ita, ba su rabuwa da ita a duk wurin da suka tsinci kansu a duniya. Wannan ya sa ko Hausawa sun yi ƙaura zuwa wasu ƙasashe da ba nasu ba, za a ga cewa suna nan tare da al’adunsu muhimmai sai ɗan abin da ba a rasa ba. Misali, idan ana gudanar da taron ƙasashen duniya a wata ƙasar, kuma ya kasance za a gabatar da al’adun gargajiya a yayin wannan taro, akan nemo masu sana’o’in hannu daga cikin Hausawa domin su wakilci ƙasar. A ƙasar Najeriya lallai ne a nemi Hausawa daga cikin waɗanda za su wakilci al’ummun Nijeriya kasancewarsu masu daɗaɗɗar al’ada fitatta wadda take kowa ya san ta a ƙasar. Akan nemi masu fasahar kiɗa da rawa da waƙa, da masu fitattun sana’o’in gargajiya da ya shafi fasahar hannu wadda za a gudanar nan take domin a san cewa lallai Hausawa ba cimazaune ba ne. Suna da fasahohi iri daban-daban masu taimakon rayuwarsu a kowane ɓangare ba tare da dogaro da wata al’umma ba.

.

Auna Fahimta

1. Wane dalili ke sa al’ada ta zama ta gari?
2. Ta yaya al’ada ke zama ta ƙasa?

## 3.4 Taƙaitawa

Wannan darasi ya fahinci cewa ko a cikin Hausawa kowane gida ko gari suna da irin tasu al'adar wadda take yi masu jagoranci wurin tafiyar da rayuwa. Yanayin wurin zama shi ne babban abin da ke haifar da bambancin na al'adun daga wannan zuwa wancan. Dalilin haka shi ne, tun lokacin da Hausawa suka fara yaɗuwa a ƙasar Hausa, ba a dunƙule suke wuri guda ba. Don haka, wajibi ne al'adunsu su yi tarayya a wasu ɓangarori, wani wurin kuma su bambanta. To amma dai al'adun Hausawa suna iya zama ƙarƙashin tsarin gida ko gari, kowa da irin tasa hanyar rayuwar da ya gada wurin iyaye da kakanni. Hausa.

## 3.6 Ma'anar Muhimman Kalmomi

## 3.7 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari


Bargery, G. P. (1934). *A Hausa–English Dictinary.* London: Oxford University press.

Bunza, A. M. (2006). *Gadon Feɗe Al'ada.* Lagos: Tiwal Nigeria Limited.

Ɗangambo, A. (1987). *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa.* Kano: Triumph.

Funtua, A. I. da Gusau, S. M. (ed) (2010). *Al'adu da Dabi'un Hausawa da Fulani.*
Kaduna: El-Abbas printers & Media Concept.

Sa'id, B. da wasu (ed) (2006). *Ƙamusun Hausa na Jami'ar Bayero*. Zaria: Ahmadu Bello University press Ltd.

Nwankpa, F. N. (2006). *Nigerian Peoples and Cultures.* Sokoto: First Standard Press.

## 3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1- Wane dalili ke sa al'ada ta zama ta gari?

Al'ada tana iya zama ta gari duka bisa la'akari da wurin zama tare da yanayin muhalli ko tushensu bisa zuriya. Wannan zai samar da al'ada wadda kowa ke bi a dukkannin ɓangarorin rayuwarsu. Misali, galibin mutanen Arugungu masunta ne. Sun gaji sana'ar Su da iya ruwa. Don haka, mutanen garin suna da al'ada ta bai ɗaya, kafin daga bisani su haɗu da mutanen da ba Argungawa ba masu al'ada ta daban da tasu. A dubi mutanen Zariya waɗanda ake kira Zage-zagi, fitaccen abincinsu na gargajiya shi ne Fate. Su kuwa Zamfarawa sun gaji abinci mai suna Hoce.

**2-** Ta yaya al'ada ke zama ta ƙasa?

A duk wurin da za a haɗu cikin ƙasar domin yin wani taro, kowa ƙoƙarinsa shi ne ya nuna hanyar rayuwarsa da ya gada iyaye da kakanni wadda ya iya. Al'adar da aka tabbatar da ita ce fitacciya ga kowace al'umma, tana iya zama al'adar da ke iya wakiltar ƙasa a lokacin wani taron buki na ƙasa ko duniya. Misali, ƙasar Hausa a jumlace al'adarsu ta fuskar tattalin arziƙi ita ce sana'ar noma, sai kasuwanci. Kowane yanki na ƙasar da irin abin da suke nomawa wanda ya yi daidai da yadda yanayin ƙasar wurin take. Wannan shi ne tushen bambance-bambance ta fuskar al'adu a ɓangaren abinci da sutura da tsarin muhalli, da kasuwanci.

## KASHI NA HUƊU MATAKAN WANZAR DA AL'ADA ABUBUWAN DA KE CIKI

### Abubuwan Da Suke Ciki

4.1 Gabatarwa
4.2 Manufar Darasi
4.3 Matakan wanzar da al'ada abubuwan da ke ciki
- 4.3.1 Raya Al'da
- 4.3.2 Bunƙasa
- 4.3.3 Yaɗuwa
- 4.3.4 Gurɓatar Al'adu
- 4.3.5 Mutuwar Al'ada
- Auna Fahimta

4.4 Taƙaitawa
4.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi
4.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
4.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

### 4.1 Gabatarwa

Wannan darasi zai dubi yadda al'ada ke samuwa ne a matsayin abu mai rai wanda idan an tattala ta, tana iya rayuwa ta bunƙasa ta bazu cikin al'umma. Idan kuma al'ada ta rayu ta bunƙasa me ke sa ta mutu. Mataki ne da za a ga yanayin da al'adar kowace al'umma ke iya shiga in har tana rayuwa.

### 4.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- Yadda ake raya al'ada.
- Dalilan gurɓatar al'ada.
- Hanyoyin yaɗuwar aladun Hausawa.

## 4.3 Matakan wanzar da al'ada abubuwan da ke ciki

### 4.3.1 Raya Al'da

Duk wani abu mai rai ko wanda ake tunanin cewa yana da siga irin ta sauran abubuwa masu rai, akwai hanyar da ake bi domin ganin cewa ya ci gaba da wanzuwa; ko da kuwa al'adarsa a ƙashe zai mutm. Hanyar da ake bi wurin raya al'ada Bahaushiya ita ce aiwatar da ita yadda take a lokaci da muhallin aiwatar da ita. Daga lokacin da Hausawa suka kula da al'ada suka yi ta, za su ga amfaninta, in har sun yi ta kamar yadda iyaye da kakanni suka yi. Bin irin wannan hanya da aiwatarwa lokaci-lokaci shi ne raya al'ada. Rashin aiwatar da al'ada ga mai ita zai sa ta daina wanzuwa. Cikin zantukan hikimar Hausa ana cewa: ''Rai dangin Goro, ruwa ake ba shi''. Ke nan idan ana son al'ada ta wanzu a matsayin hanyar rayuwa mai ɗorewa, to ya zama wajibi a kula da ita. Kula da al'ada ba zai yiwu ba, sai ana aiwatarwa.

Gusau (2010: 2) yana cewa: "Al'adun al'umma, abubuwa ne masu rai waɗanda sukan shafi dangogin rayuwa daban-daban. Wannan zance ya tabbatar da al'ada a matsayin wani abu mai rai da ake gudanarwa a ɓangarorin rayuwa. Misali, al'adar 'Tashe' ga Hausawa har yanzu tana raye, saboda duk lokacin azumi akan gudanar da ita. Ba ma Tashe ba, sauran dangogin al'adun Hausawa irin su tashe (tashin mutum daga barci) domin yin sahur, da sauyin abinci lokacin azumi, da yawan yin abadoji, da sadaka suna nan ba a daina yi ba.

### 4.3.2 Bunƙasa

Al'ada idan tana rayuwa a wurin masu gudanar da ita, za ta bunƙasa ta zama babba. Hanyar rayuwa idan ta sami karɓuwa, abin da ke biyo bayanta shi ne ta ƙara inganta dangane da yadda ake aiwatar da ita. Irin wannan ake kira bunƙasa. Za a riƙe ta hannu bibiyu, masu yin ta za su yawaita. Misali, al'adar noma a wurin Hausawa da ta daɗe a raye, kullum ƙara bunƙasa take. Waɗanda suke yin kaɗan, yanzu suna yi da yawa. Masu yi ba tare da cikakken kulawa ba, sun ba abin muhimmanci saboda samun abinci da kuɗin kashewa.

### 4.3.3 Yaɗuwa

A duk inda Hausawa suke suna tare da al'adunsu. Wannan ya sa al'adar Hausawa ta yaɗu ƙwarai a sassan duniyar da ba ta Hausawa ba. Raya al'ada a wurin Hausawa, shi ya kawa yaɗuwarta a sassa da ba nasa ba. Akwai hanyoyi da dama da suka zama sila ta yaɗuwar al'adun Hausawa. Adamu (1976) ya yi bayanin al'adun Hausawa da suka yaɗu a

yammacin Afirka tare da hanyoyi ko dalilan yaɗuwarsu. A cewar Adamu (1976) fataucin Hausawa daga ƙasar Hausa zuwa Gwanja, da jihadin daular Usmaniyya, da kasuwancin Hausawa, da maƙwabta, da ƙaurar Hausawa daga ƙasar Hausa zuwa yammacin Afirka domin neman ilimi, sun taka ruwa wurin yaɗuwar al'adun Hausawa. Waɗannan dalilai, sun nuna cewa duk lokacin da Hausawa suka bar ƙasar Hausa zuwa ƙasar da ba tasu ba, tafe suke da al'adunsu da suka shafi zamantakewa da abinci da sutura da kiwon lafiya da harshe da ban gaskiya.

### 4.3.4 Gurɓatar Al'adu

Al'adun kowace al'umma idan sun bunƙasa, za su yaɗu a sauran nahiyoyin da ba nan ne asalin masu al'adar ba. Idan al'ada ta yaɗu daga wurin da masu ita suke na asali, abu na gaba shi ne a ga ana gudanar da al'adar cikin tsarin da haka ake yi ba a muhallinta na asali. A nan, dole a sami sauyi ta fuskar ragi ko ƙari daga yadda al'ada take. Da zarar al'ada ta fuskanci wannan ɓarazana, ya zama wajibi ta gurɓace. Gurɓatar al'ada tana nufin cakuɗa al'ada zaunanna da aka sami da wasu baƙin lamura waɗanda babu su a da can kamar yadda aka gaji abin wurin iyaye da kakanni. Misali, al'adar taron suna wanda mata ke yi a yanzu, ta gurɓata sakamakon sauyin da ya shigo ciki. Sauyin shi ne, aiwatar da bukin da canje-canje na ragi ko ƙari daga yadda aka saba yi. A maimakon raba Ragon suna bisa al'ada wanda kowane sashe na Ragon akwai wanda ake ba bisa al'ada, ana yanka shi ne a dafa a rabar da shi ga duk wanda ya zo bukin. Irin wannan ya fi faruwa a muhallin da Hausawa suka bar gida, ko da kuwa a tsakaninsu Hausawa mazauna wannan wurin aka yi bukin.

A ɓangaren aure, al'adun da aka saba da su, wasunsu sun gurɓata. An daina bukin baiko a wasu wuraren, sai dai a raba wasu kayayyaki da za su nuna an yi baikon ɗauke da lokacin da za a yi bukin. Wasan hawan Sallah wanda Sarakuna suke yi, yanzu ya zama wurin da husuma ke iya tashi tsakanin matasa daga unguwanni daban-daban, da dai sauransu.

### 4.3.5 Mutuwar Al'ada

Duk abin da aka ce ya mutu, to ana nufin ya daina rayuwa gaba ɗaya. Kasancewa tun al'ada tana raye, ta ci gaba har ta bunƙasa zuwa gurɓata; ba abin mamaki ba ne ta mutu. Mutuwar al'ada yana samuwa ne a lokacin da masu ita suka daina yin ta, ko zuriyarsu ta ƙare, ko kuma al'adar ta gurɓata zuwa wani abu daban wanda ba wannan abu da aka gada ba. A irin haka, al'ada ta mutu. Idan kuma aka musaya al'ada da wata rayuwa musamman wayewa ko ci gaban zamani, wannan shi ma yana kawo mutuwar al'ada.

Auna Fahimta

1- Me ke sa al'ada ta yaɗu?
2- Waɗanne dalilai ke kawo gurɓatar al'ada.

## 4.4 Taƙaitawa

Wannan darasi ya dubi yadda al'adun Hausawa suke rayuwa ne har ya zuwa mutuwa. An dubi matakan da al'ada ke hawa na rayuwa da bunƙasa da yaɗuwa, kafin ta gurɓata. A taƙ aice al'ada tana iya wanzuwa, ta gushe in dai ta yaɗu.

## 4.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi

## 4.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari


Bargery, G. P. (1934). *A Hausa–English Dictinary.* London: Oxford University press.

Bunza, A. M. (2006). *Gadon Feɗe Al'ada.* Lagos: Tiwal Nigeria Limited.

Ɗangambo, A. (1987). *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa.* Kano: Triumph.

Gusau, S. M. (2008). *Waƙar Baka a ƙasar Hausawa: Yanaye-Yanayensu da Sigoginsu.* Kano: Bench Mark Pulishers

Funtua, A. I. da Gusau, S. M. (ed) (2010). *Al'adu da Dabi'un Hausawa da Fulani.* Kaduna: El-Abbas printers & Media Concept.

Sa'id, B. da wasu (ed) (2006). *Ƙamusun Hausa na Jami'ar Bayero*. Zaria: Ahmadu Bello University press Ltd.

## 4.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1- Me ke sa al'ada ta yaɗu?

A duk inda Hausawa suke suna tare da al'adunsu. Wannan ya sa al'adar Hausawa ta yaɗu ƙwarai a sassan duniyar da ba ta Hausawa ba. Raya al'ada a wurin Hausawa, shi ya kawa yaɗuwarta a sassa da ba nasa ba. Akwai hanyoyi da dama da suka zama sila ta yaɗuwar al'adun Hausawa. Hanyoyi ko dalilan yaɗuwar al'adun Hausawa sun haɗa; fataucin Hausawa daga ƙasar Hausa zuwa Gwanja, da jihadin daular Usmaniyya, da kasuwancin Hausawa, da maƙwabta, da ƙaurar Hausawa daga ƙasar Hausa zuwa yammacin Afirka domin neman ilimi, sun taka ruwa wurin yaɗuwar al'adun Hausawa. Waɗannan dalilai, sun nuna cewa duk lokacin da Hausawa suka bar ƙasar Hausa zuwa ƙasar da ba tasu ba, tafe suke da al'adunsu da suka shafi zamantakewa da abinci da sutura da kiwon lafiya da harshe da ban gaskiya.

2- Waɗanne dalilai ke kawo gurɓatar al'ada.

Duk abin da aka ce ya mutu, to ana nufin ya daina rayuwa gaba ɗaya. Kasancewa tun al'ada tana raye, ta ci gaba har ta bunƙasa zuwa gurɓata; ba abin mamaki ba ne ta mutu. Mutuwar al'ada yana samuwa ne a lokacin da masu ita suka daina yin ta, ko zuriyarsu ta ƙare, ko kuma al'adar ta gurɓata zuwa wani abu daban wanda ba wannan abu da aka gada ba. A irin haka, al'ada ta mutu. Idan kuma aka musaya al'ada da wata rayuwa musamman wayewa ko ci gaban zamani, wannan shi ma yana kawo mutuwar al'ada.

**RUKUNI NA 2 AL'ADA A TUNANIN HAUSAWA**

Kashi Na 1 Jin Dađi
Kashi Na 2 Tattalin Arziƙi
Kashi Na 3 Addini
Kashi Na 4 Shugabanci

**KASHI NA 1 JIN DAƊI**

**Abubuwan da suke ciki**

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufar Darasi
1.3 Jin dađi
 1.3.1 Kađe-Kađe
 1.3.2 Raye-Raye
 1.3.3 Waƙe-Waƙe
 1.3.4 Bukukuwa
 Auna Fahimta
1.4 Taƙaitawa
1.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi
1.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



## 1.1 Gabatarwa

Jin dađi ɓangare ne daga cikin abubuwan da Hausawa suke đauka a matsayin al'ada. Wannan darasi zai dubi wasu ɓangarori ne na cikin adabin Hausa a idon manazarta al'adun Hausa a matsayin abin da aka gada iyaye da kakanni a matsayin hanyar rayuwa a wasu ɓangarori na rayuwar Hausawa masu zama al'adu a ɓangaren nazarin al'ada.



## 1.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- Mene ne jin dađi?
- Yadda jin dađi ya rikiđe daga adabi zuwa al'ada.
- Muhallan aiwatar da kiđa da waƙa da wasanni.

## 1.3 Jin daɗi

### 1.3.1 Kaɗe-Kaɗe

Kaɗe-kaɗe sassan adabi ne, amma kasancewarsu wata fasaha kuma hanyar gudanar da rayuwar Hausawa da ake yi da nufin samar da nishaɗi da jin daɗi, ya zama al'ada. Sa'id da Wasu (2006:243) sun bayyana kiɗa da cewa bugun ganga ko kalangu da abin busawa ko bugun ƙwarya ko goge ko garaya da hannu ko da makaɗi, ko da wani abu. Ta yin la'akari da wannan ma'ana, kiɗa shi ne samuwar wani amo da zai sanya jin daɗi a sakamakon kaɗawa ko gogawa ko girgizawa ko ƙyanƙyasawa na wani abin kiɗa da nufin isar da saƙo ko domin aiwatar da waƙa. Kiɗa a wurin Hausawa al'ada ce da aka gada tun ga iyaye da kakanni.

Gusau (2008) yana ganin tarihin kiɗa ya nuna cewa Hausawa sun fara amfani da kiɗa ne ta hanyar busa ƙaho da nufin sadarwa. Idan kuwa haka ne, kiɗa wata hanya ce da aka taso da ita wadda ake yin rayuwa a duk lokacin da aka shiga daji wurin farauta, ko ana zaune gida da nufin sadarwa a tsakanin 'yan'uwa. Wannan hanya tun daga lokacin da Hausawa suke zama irin na da, har yanzu tana raye. Haka kuma, kaɗe-kaɗen Hausawa sun rabu zuwa gidaje. Kowane rukunin jama'a yana da masu yi masu kiɗa da kayan kiɗa na musamman. A al'adance, wani kayan kiɗan, ba a yi wa wani rukuni na jama'a kiɗa da su.

### 1.3.2 Raye-Raye

Rawa shi ne kaɗa jiki da girgiza shi da rausaya don annashuwa da nishaɗi, musamman in akwai kiɗa, a cewar Sa'id da Wasu (2006). Wannan bayanin nasu ya ƙara fito da rawa a matsayin jin daɗi da ke samar da nishaɗi idan ya zo tare da kiɗa. Shi kuwa jin daɗi nau'in rawa hanya ce ta rayuwar Hausawa a duk lokacin da aka wasu hidindimu na nuna farin ciki. Hausawa sun gaji rawa, sun iya, sun saba yin ta. Don haka ne ma suke da rawar Asawwara, da rawar ƙoroso, da dai sauransu.

### 1.3.3 Waƙe-Waƙe

Waƙa zance ne na hikima da ake tsarawa cikin azanci ta hanyar rerawa. Gusau (2011:11) yana cewa waƙar baka ita wadda take zaburar da al'umma tare kuma da karkatar da ita zuwa ga dabarun tafiyar da rayuwa da za su ba da damar a cim ma gaga mai inganci. Ma'anar tasa ta fito da ƙunshiyar waƙar baka a matsayin al'adar Hausawa. Ya ce waƙar baka tana taimakawa wurin samun dabarun tafiyar da rayuwa. Ke nan duk wata hanya da aka gada wadda take tafiyar da rayuwa da ke

gudana cikin jin daɗi, ya wuce adabi kaɗai, al'da ce ta masu yin wannan rayuwa.

Waƙa a matayin jin daɗi kuma al'ada ana samunta a ɓangarori masu yawa. Akwai mawaƙan fada, da na jama'a, da na maza, da na yara, da na mata, da na raino, da na daka, da dai sauransu. Mafi yawan waƙoƙin baka na Hausa ana aiwatar da su ne a wurare ko ga masu tafiyar da wata rayuwa da suka gada wurin iyaye da kakanni. Misali, waƙoƙin daɓe da na daka da na niɗa da na reno dana fada da na cikin tatsuniyoyi da dai sauransu. Galibin makaɗa da mawaƙan Hausa ba haye suke yi ba, sun gaji abin ne wurin iyaye da kakanni. Idan kuwa haka ne, ana iya kiran gadon aiwatar da kiɗa da waka da cewa gadon gudanar da al'ada a matsayin gado kamar yadda masu sana'o'in gargajiya suke yi.

### 1.3.3 Bukukuwa

Buki taro ne na shagali domin nuna farin ciki wajen aure ko suna ko naɗin sarauta ko salla ko al'adun gargajiya, a cewar Sa'id da Wasu (2006). Hausawa suna gudanar da bukukuwa iri daban-daban a matakan rayuwa da sauran harkokin yau da kullum. Bukukuwan Hausawa sun gaje su ne wurin iyaye da kakanni a matsayin hanyar gudanar da rayuwa da za a riƙa yi a duk wasu lokuta in sun zagayo, ko idan wani abu ya faru. Akwai bukukuwan da Hausawa suke gudanarwa da kakar kowace shekara. Misali, bukin kalankuwa da bukin bauta na shekara da bukin masu sana'o'in gargajiya, da bukin bazara na gida ko zuriya ga abin ban gaskiya.

Auna Fahimta

1- Yi bayani biyu daga cikin waɗannan: -
2- Me ake nufi da bukukuwan Hausawa?



## 1.5 Taƙaitawa

Darasin ya yi bayanin wani ɓangare daga cikin abubuwan da Hausawa suke gani a matsayin jin daɗi kuma hanyar gudanar da rayuwa. To sai dai, a lura cewa ba su kaɗai ba ne hanyoyin jin daɗi da ke zama a matsayin al'ada ba. Ana iya samun wasu abubuwan fiye da haka.

## 1.6 Ma'anar Muhimman Kalmomi

Rawa: - shi ne kaɗa jiki da girgiza shi da rausaya don annashuwa da nishaɗi, musamman in akwai kiɗa.

## 1.7 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

Bargery, G. P. (1934). A Hausa–English Dictinary. London: Oxford University press.

Bunza, A. M. (2006). Gadon Feɗe Al'ada. Lagos: Tiwal Nigeria Limited.

Ɗangambo, A. (1987). Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa. Kano: Triumph.

Gusau, S. M. (2008). Waƙar Baka a ƙasar Hausawa: Yanaye-Yanayensu da Sigoginsu.
Kano: Bench Mark Pulishers

Funtua, A. I. da Gusau, S. M. (ed) (2010). Al'adu da Dabi'un Hausawa da Fulani.

Kaduna: El-Abbas printers & Media Concept.

Sa'id, B. da wasu (ed) (2006). Ƙamusun Hausa na Jami'ar Bayero. Zaria: Ahmadu Bello University press Ltd.

## Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1- Yi taƙaitaccen bayani kan biyu daga cikin waɗannan: -
i- Kaɗe-Kaɗe
ii- Raye-raye
iii- Waƙe-waƙe

- Kaɗe-kaɗe

Sassan adabi ne, amma kasancewarsu wata fasaha kuma hanyar gudanar da rayuwar Hausawa da ake yi da nufin samar da nishaɗi da jin daɗi, ya zama al'ada. Kiɗa shi bugun ganga ko kalangu ko abin busawa ko bugun ƙwarya ko goge ko garaya da hannu ko da makaɗi, ko da wani abu. Ta yin la'akari da wannan ma'ana, kiɗa shi ne samuwar wani amo da zai sanya jin daɗi a sakamakon kaɗawa ko gogawa ko girgizawa ko ƙyanƙyasawa na wani abin kiɗa da nufin isar da saƙo ko domin aiwatar da waƙa. Kiɗa a wurin Hausawa al'ada ce da aka gada tun ga iyaye da kakanni.

- Raye-Raye

Rawa shi ne kaɗa jiki da girgiza shi da rausaya don annashuwa da nishaɗi, musamman in akwai kiɗa. Shi kuwa jin daɗi nau'in rawa hanya ce ta rayuwar Hausawa a duk lokacin da aka wasu hidindimu na nuna farin ciki. Hausawa sun gaji rawa, sun iya, sun saba yin ta. Don haka ne ma suke da rawar Asawwara, da rawar ƙoroso, da dai sauransu.

- Waƙe-Waƙe

Waƙa zance ne na hikima da ake tsarawa cikin azanci ta hanyar rerawa. Waƙar baka ita wadda take zaburar da al'umma tare kuma da karkatar da ita zuwa ga dabarun tafiyar da rayuwa da za su ba da damar a cim ma gaga mai inganci. Ma'anar tasa ta fito da ƙunshiyar waƙar baka a matsayin al'adar Hausawa. Ya ce waƙar baka tana taimakawa wurin samun dabarun tafiyar da rayuwa. Ke nan duk wata hanya da aka gada wadda take tafiyar da rayuwa da ke gudana cikin jin daɗi, ya wuce adabi kaɗai, al'da ce ta masu yin wannan rayuwa.

2- Me ake nufi da bukukuwan Hausawa?

Buki taro ne na shagali domin nuna farin ciki wajen aure ko suna ko naɗin sarauta ko salla ko al'adun gargajiya. Hausawa suna gudanar da bukukuwa iri daban-daban a matakan rayuwa da sauran harkokin yau da kullum. Bukukuwan Hausawa sun gaje su ne wurin iyaye da kakanni a matsayin hanyar gudanar da rayuwa da za a riƙa yi a duk wasu lokuta in sun zagayo, ko idan wani abu ya faru. Akwai bukukuwan da Hausawa suke gudanarwa da kakar kowace shekara. Misali, bukin kalankuwa da bukin bauta na shekara da bukin masu sana'o'in gargajiya, da bukin bazara na gida ko zuriya ga abin ban gaskiya.

## KASHI NA BIYU TATTALIN ARZIƙI

### Abubuwan da suke ciki


2.1 Gabatarwa
2.2 Manufar Darasi
2.3 Ma'anar tattalin Arziƙi
2.3.1 Hanyoyin Bunƙasa Tattalin Arziƙi.
2.3.1.1Sana'a
2.3.1.2Kasuwanci
2.3.1.3Aikatau ko ƙwadagoAuna Fahimta
2.4 Taƙaitawa
2.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi
2.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta




### 2.1 Gabatarwa

Hanyoyin da kowace al'umma take bi domin samun abinci suna dogara ne da irin muhallin da ake zaune ciki. Irin wannan ya kawo bambance-bambance dangane da nau'o'in abinci a tsakanin mazauna yankuna daban-daban. Cikin al'ummar Hausawa, akwai hanyoyin da suke amfani da su domin neman abinci da kayayyakin ayyukan gida ko noma da farauta da cinikayya ta hanyar kasuwanci, da kuma hanyoyin da suke bi domin yin aikin ƙarfi domin samun kuɗin biyan buƙata. Za a yi bayanin hanyoyin da Hausawa suke bi domin samun abinci, da kuɗi waɗanda gado ne suka yi, kuma tsari ne na tafiyar da rayuwa wanda ya zama al'ada ga Hausawa.



### 2.2 Manufofin Darasi

- A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci: Sanin ko mene ne tattalin arziƙi
- Gane bambancin sana'a da kasuwanci
- Iya gane sigogin aikatau ko ƙwadago

## 2.3 Ma'anar tattalin Arziƙi

Tattalin arziki a cewar Auta (2006:196) tsari ne na sarrafa albarkatun ƙasa da sauran ni'imomin da Allah ya yi wa ɗan Adam domin samar da muhimman abubuwa da rarraba su ga jama'a masu buƙata. Nuhu (2019:3) ya bayyana tattalin arziƙi da cewa hanya ce ta sarrafa albarkatun ƙasa domin a samar da abinci da abubuwan da kan taimaka a tafiyar da rayuwa, da yin saye da sayarwa a sami riba, da yin aikin ƙwadago cikin yini ko a yi jinga da wasu a biya kuɗi. A taƙaice tattalin arziƙi hanyoyin da al'umma ke bi ko dogara da su domin samun abinci ko kayan aki da ciniki da aikatau.

### 2.3.1 Hanyoyin Bunƙasa Tattalin Arziƙi.

Wannan hanyoyi da Hausawa suke bi domin bunƙasar tattalin arziƙi, gadonsu ake yi wurin iyaye da zuriya. Ke nan abin ya zama gargajiya saboda sana'o'i ne da kasuwanci wanda iyaye da kakanni suke bi domin samun abinci da kuɗi. Hanyar yin kowane ɗan gida su zai koya idan ya taso domin samun kuɗi ko abinci, da riƙe gadon gida. Waɗannan hanyoyi su ne:

#### 2,3.1.1 Sana'a

Sarrafa albarkatun ƙasa domin samun abinci ko wasu kayayyakin da za su taimaka wurin gudanar da rayuwar yau da kullum shi ne sana'a. Sana'o'in Hausawa na gargajiya gadonsu ake yi wurin iyaye. Yara suna koyo, ana koya masu tun suna ƙanana har su iya. Sukan naƙalci duk wata al'ada da ta shafi wannan sana'a. Sana'o'in Hausawa wanda suka gada wurin iyaye da kakanni suna da yawa. Daga cikinsu akwai:

a. Noma.
b. ƙira.
c. Saƙa.
d. Jima
e. Rini
f. Su
g. Dukanci
h. Gini
i. Fawa
j. Wanzanci

Irin waɗannan sana'o'i da Hausawa suke gudanarwa suna da dogon tarihi, ana samun gidajen da suka gaji wata sana'a wadda ita ke riƙe da su na tsawon rayuwa. Da wannan sana'ar suke ci, suke sha, da sauran lalurorin yau da kullum.

#### 2.3.1.2 Kasuwanci

Kasuwanci shi ne saye da sayarwa a kasuwa, a cewar Sa'id da wasu (2006:238). A saya a sayar domin a ci riba hanya ce ta samun kuɗi wadda Hausawa suke yi domin sun taso cikinta. Hakan ya sa rayuwar Hausawa ta wanzu a wasu sassa na wajen ƙasar Hausa, a cewar Adamu (1979). Fitattun kasuwancin Hausawa da aka san su da shi su ne: Saye da sayar da goro, da dabbobi ta hanyar fatauci wanda suke yi daga ƙasar Hausa zuwa Gwanja. Hausawa sun gaji kasuwancin hatsi, da kayan lambu, da sauransu.

#### 2.3.1.3 Aikatau ko ƙwadogo

Aikatau ko ƙwadago shi ne yi wa wani aiki don ya biya kuɗi, musamman aikin gona wadda take da ma'ana daidai da aikatau ko barema, a cewar Sa'id da wasu (2006:289). Aikatau ko ƙwadago hanya ce ta samun kuɗi wadda Hausawa suka mayar hanyar rayuwarsu da suke bi domin dogaro da kai. Sukan yi aiki na yini ko safiya ko yammaci, ko a yi jingar aiki dukansa bisa wasu kuɗi da aka yi yarjejeniya. Wannan hanyar rayuwa ta daɗe cikin al'ummar Hasawa a matsayin abin da mutum zai dogara da shi wurin riƙe iyali, da yin duk wasu lalurori na rayuwa

Auna Fahimta

1- Mene ne tattalin arzƙi?
2- Waɗanne sana'o'i ne suke samar da kayayyakin aiki?



## 2.4 Taƙaitawa

Hanyoyin tattalin arziƙin Hausawa sun nuna cewa sana'o'i da kasuwanci su ne muhimmai a cikin abin da Hausawa suke amfani da su domin samun abinci da kuɗi. Kowane ɓangare, ana gado ne a gida, ba haye ake yi ba.

## 2.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi

Aikatau ko ƙwadago: - shi ne yi wa wani aiki don ya biya kuɗi

## 2.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

Adamu, M. (1979). The Spread of Hausa Culture in West Afrika. In *Savanna Jounal of the Environmental and Social Sciences*. Zaria: Ahmadu Bello University press Ltd.

Auta, A. L. (2006). Tattalin Arziƙin Al'umma: Nazarin Sana'o'i Da Kasuwancin

Hausawa. A Cikin *Algaita Journal of Current Research In Hausa studies Vol. 1 No: 4.* September. Kano: Bayero University.

Bargery, G. P. (1934). A Hausa–English Dictinary. London: Oxford University press.

Bunza, A. M. (2006). Gadon Feɗe Al'ada. Lagos: Tiwal Nigeria Limited.

Ɗangambo, A. (1987). Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa. Kano: Triumph.

Gusau, S. M. (2008). Waƙar Baka a ƙasar Hausawa: Yanaye-Yanayensu da Sigoginsu.
Kano: Bench Mark Pulishers

Funtua, A. I. da Gusau, S. M. (ed) (2010). Al'adu da Dabi'un Hausawa da Fulani.
Kaduna: El-Abbas printers & Media Concept.

Nuhu, A. Tattalin Arziki Maguzawa a Rigar Zamani. Ph.D. Seminar. Department of Nigerian Languages, Sokoto: Usmanu [anfodiyo University

Sa'id, B. da wasu (ed) (2006). Ƙamusun Hausa na Jami'ar Bayero. Zaria: Ahmadu Bello University press Ltd

## 2.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1- Mene ne tattalin arzƙi?

Tattalin arziki a cewar Auta (2006:196) tsari ne na sarrafa albarkatunƙ asa da sauran ni'imomin da Allah ya yi wa ɗan Adam domin samar da muhimman abubuwa da rarraba su ga jama'a masu buƙata. Nuhu (2019:3) ya bayyana tattalin arziƙi da cewa hanya ce ta sarrafa albarkatun ƙasa domin a samar da abinci da abubuwan da kan taimaka a tafiyar da rayuwa, da yin saye da sayarwa a sami riba, da yin aikin ƙwadago cikin yini ko a yi jinga da wasu a biya kuɗi. A taƙaice tattalin arziƙi hanyoyin da al'umma ke bi ko dogara da su domin samun abinci ko kayan aki da ciniki da aikatau.

2- Waɗanne sana'o'i ne suke samar da kayayyakin aiki?

i- Noma.

ii- ƙira.

iii- Saƙa.

iv- Jima

v- Rini

vi- Dukanci

# KASHI NA 3 ADDINI

## Abubuwan da suke Ciki

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufar Darasi
3.3 Ma'anar Bautar Gargajiya
3.3.1 Abubuwan da Ake Bauta Wa
3.3.2 Wuraren Bauta
3.4 Musulunci
Auna Fahimta
3.5 Taƙaitawa
3.6 Ma'anar Muhimman Kalmomi
3.7 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
3.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



**3.1** Kowace al'umma akwai abin da ta yarda da shi a matsayin hanyar da ta bayar da gaskiya, irin wannan harya an gaje ta ne tun da daɗewa wurin magabata. Don haka ne Hausawa suke ganin duk abin da aka gada wurin iyaye da kakanni wanda addini ma yana cikinsu a matsayin al'ada. Wannan darisi zai mayar da hankali ne wurin duban hanyoyin da Hausawa suke bi domin yin bauta daga jiya zuwa yau. Hanyoyin bangare ne na rayuwa wanda suka gada wurin iyaye da kakanni. Don haka, bin wannan hanya a matsayin tafarki na rayuwa, wajibi ne saboda al'adarsu ce.



## 3.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- Sanin abin da ake nufi da bauta.
- Gane hanyoyin ban gaskiyar Hausawa ta gargajiye
- Lura da yadda al'adar ban gaskiya ke sauyawa daga gargajiya zuwa zamani.

## 3.3 Ma'anar Bautar Gargajiya

Bautar gargajiya hanya ce ta ban gaskiya da Hausawa suke amfani da ita domin yi wa Iskoki hidima da kiyaye wasu dokoki nasu domin su sami biyan bunƙata daga garesu. Hanyoyin da Hausawa suke bi wurin hidimomin su ne yin yanke-yanken dabbobi, da aikata wasu halaye ko barin yin wani abu wanda Iskokin suke so a yi. Masu yin waɗannan ayyuka suna sa ran ganin sakamakon aikata wannan aiki. Saɓa dokokin kuma yana tattare da ganin sakamako mummuna ga wanda ya aikata hakan.

Irin wannan hanyar rayuwa ga Hausawa daɗaɗɗa ce da har yanzu akwai masu aiwatar da ita. Dalili aiwatarwar shi ne, abin da suka gada a matsayin hanyar rayuwa. Don haka abin yake gargajiya kuma al'ada wadda aka saba aka tashi da ita.

### 3.3.1 Abubuwan da Ake Bauta Wa

Cikin tsarin bautar gargajiya da Hausawa suke bi a matsayin hanyar rayuwa, Iskoki ne ake yi wa hidima musamman da bazara. Baya ga lokacin bazara, ana yin wasu hidindimun a duk lokacin da buƙata ta taso. Greenber (1947) da Ibrahim (1982) da Bunza (2006) sun bayyana cewa Iskokin da ake yi wa bauta a gargajiyance sun rabu zuwa gida biyu kamar haka:

a. Fararen Iskoki.
b. Baƙaƙen Iskoki

Fararen Iskoki a cewarsu su ne waɗanda ba sa cutarwa, ana yin zaman lumana da su. Misali, Malam Alhaji, da Balarabe, da [angaladima, da sauransu. Ana hulɗa da su, ba tare da matsala ba. Baƙaƙen Iskoki su ne masu cutarwa, ba su da sabo, su ne masu sauya cutuka na rashin lafiya ga mutum. Misali, Inna da Bagiro, da Kure, da Duna, da Nakada da Gajimare da dai sauransu.

### 3.3.2 Wuraren Bauta

Bautar Iskoki ana yin ta ne a wasu wurare na musamman wanda aka tabbatar cewa Iskar da ake yi wa bauta tana zama wurin. Bunza (2006) ya yi bayanin dabbobi, da tsirrai, da itatuwa, da ramu, da gulabe a matsayin wuraren zaman Iskoki. To sai dai ba kowannensu ba ne wurin bauta. Akan keɓe wata itaciya da za a riƙa yin bautar ne kamar tsamiya ga masu bautar Bagiro. Suna kiran wannan tsamiya da suna Gunki, wato wurin da ake bautar Iska Bagiro.

Nuhu (2020) ya bayyana cewa wasu Hausawan suna amfani da wani dutse ne a matsayin wurin yin bautarsu. Dutse kuwa daman yana daga cikin wuraren da Iskoki suke zama. Misali, dutsen Dala da ke Kano an yi bautar 'Tsunburbura' a kansa. Dutsen [antalle da ke Birchi Maguzawan Kainafara sun yi bautar 'Mai Gemamu Ta [antalle' a cikinsa. Dutsen Kwatarkwashi, an yi bauta kansa. Baya ga haka, masu bautar Iskar Uwargona. Suna ayyana wasu duwatsu masu sigar murhu da wani kari a sama, matsayin wurin bautar Iska Uwargona.

## 3.4 Musulunci

Kafin bayyanar addinin Musulunci ga Hausawa, suna cikin rayuwar Maguzawa ne. kowace al'umma a iya cewa ta yi Maguzanci kafin ta amshi Musulumci. Musulumci, shi ne yarda da Allah (S.W.A) a matsayin Mahalicci, a shaida Annabi Muhammadu manzonsa ne, da yin Sallah, da fitar da Zakka, da zuwa aikin Hajji idan an samu hali. Yahya (1988) ya bayyana cewa addinin Musulumci ya shigo ƙasar Hausa daga Larabawa 'yan kasuwa da Malamai Wangarawa, ya sauya tunanin Hausawa daga ban gaskiyar Iskoki zuwa saukakken addini.

Wannan sabuwar hanya da Hausawa suka samu daga baya, ta sauya rayuwa daga yadda suke a gargajiyance zuwa yau. A maimakon ban gaskiya da Iskoki, sai aka koma bin Allah da dokokinsa. Yawancin rayuwar Hausawa ta yanzu, ana yin ta ne cikin al'adun Musulumci. A wurin Hausawan yanzu, Ibadojinsu suna zaman ɓangare na al'adunsu.

Auna Fahimta

1. Mece ce bautar gargajiya?
2. Yaya wuraren bautar gargajiya suke?
3. Waɗanne dalilai ke sa al'adar bangaskiya ta sauya daga gargajiya zuwa zamani?

## 3.5 Taƙaitawa

Wannan fasali bayani ne na addinin Hausawa a matsayin hanyar da suka gada tun iyaye da kakanni zuwa yau. Hanya ta farko saura kaɗan ta gushe, Musulunci ya maye gurbinta. Ana iya cewa al'adun gargajiyar Hausawa zalla suna ta gushewa, yanzu al'adun Musulunci sun fi rinjaye.

### 3.6 Ma'anar Muhimman Kalmomi

Bautar gargajiya: - hanya ce ta ban gaskiya da Hausawa suke amfani da ita domin yi wa Iskoki hidima da kiyaye wasu dokoki nasu domin su sami biyan bunƙata daga garesu.

### 3.7 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

Adamu, M. (1979). The Spread of Hausa Culture In West Afrika. In *Savanna Jounal of the Environmental and Social Sciences*. Zaria: Ahmadu Bello University press Ltd.

Auta, A. L. (2006). Tattalin Arziƙin Al'umma: Nazarin Sana'o'i Da Kasuwancin

Hausawa. A Cikin *Algaita Journal Of Current Research In Hausa studies Vol . 1 No: 4.* September. Kano: Bayero University.

Bargery, G. P. (1934). A Hausa–English Dictinary. London: Oxford University press.

Bunza, A. M. (2006). Gadon Feɗe Al'ada. Lagos: Tiwal Nigeria Limited.

Ɗangambo, A. (1987). Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa. Kano: Triumph.

Funtua, A. I. da Gusau, S. M. (ed) (2010). Al'adu da Dabi'un Hausawa da Fulani.
Kaduna: El-Abbas printers & Media Concept.

Greenber, J. (1947). *The Influence of Isam on a Sudaness Religion. Monograph of the American Ethnological society.* New York: J.J Augustin publishers.

Gusau, S. M. (2008). Waƙar Baka a ƙasar Hausawa: Yanaye-Yanayensu da Sigoginsu.
Kano: Bench Mark Pulishers

Ibrahim, M. S. (1982). Dangantakar Al'ada da Addini: Tasirin Musulunci a Rayuwar

Hausawa ta Gargajiya Kundin Digiri na Biyu, sashen Harsunan Nigeria. Kano: Jami'ar Bayero.

Nuhu, A. Tattalin Arziki Maguzawa a Rigar Zamani. Ph.D. Seminar. Department of Nigerian Languages, Sokoto: Usmanu [anfodiyo University

Sa'id, B. da wasu (ed) (2006). Ƙamusun Hausa na Jami'ar Bayero. Zaria: Ahmadu Bello University press Ltd.

Yahaya, I. Y. 1988. *Hausa a Rubucea. Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa.* Zaria:
Northern Nigerian Publication campany Limited.

## 3.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1- Mece ce bautar gargajiya?

Bautar gargajiya hanya ce ta ban gaskiya da Hausawa suke amfani da ita domin yi wa Iskoki hidima da kiyaye wasu dokoki nasu domin su sami biyan bunƙata daga garesu. Hanyoyin da Hausawa suke bi wurin hidimomin su ne yin yanke-yanken dabbobi, da aikata wasu halaye ko barin yin wani abu wanda Iskokin suke so a yi. Masu yin waɗannan ayyuka suna sa ran ganin sakamakon aikata wannan aiki. Saɓa dokokin kuma yana tattare da ganin sakamako mummuna ga wanda ya aikata hakan.

2- Yaya wuraren bautar gargajiya suke?

- i- Tsirrai
- ii- Itatuwa
- iii- Ramu
- iv- Gulabe

3- Waɗanne dalilai ke sa al'adar bangaskiya ta sauya daga gargajiya zuwa zamani?

Kafin bayyanar addinin Musulunci ga Hausawa, suna cikin rayuwar Maguzawa ne. kowace al'umma a iya cewa ta yi Maguzanci kafin ta amshi Musulumci. Musulumci, shi ne yarda da Allah (S.W.A) a matsayin Mahalicci, a shaida Annabi Muhammadu manzonsa ne, da yin Sallah, da fitar da Zakka, da zuwa aikin Hajji idan an samu hali. Addinin Musulumci ya shigo ƙasar Hausa daga Larabawa 'yan kasuwa da Malamai Wangarawa, ya sauya tunanin Hausawa daga ban gaskiyar Iskoki zuwa saukakken addini.

Wannan sabuwar hanya da Hausawa suka samu daga baya, ta sauya rayuwa daga yadda suke a gargajiyance zuwa yau. A maimakon ban gaskiya da Iskoki, sai aka koma bin Allah da dokokinsa. Yawancin rayuwar Hausawa ta yanzu, ana yin ta ne cikin al'adun Musulumci. A wurin Hausawan yanzu, Ibadojinsu suna zaman ɓangare na al'adunsu.

# KASHI NA 4 SHUGABANCI

## Abubuwan da suke Ciki

4.1 Gabatarwa
4.2 Manufar Darasi
4.3 Shugabanci
    4.3.1 Maigida
    4.3.2 Mai unguwa
    4.3.3 Dagaci
    4.3.4 Hakimi
    4.3.5 Sarki
    Auna Fahimta
4.4 Taƙaitawa
4.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi
4.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
4.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



## 4.1 Gabatarwa

Wannan sashe zai dubi tsarin da Hausawa suke da shi wanda yake tafiyar da jagorancin al'umma mataki-mataki. A nan, za a yi bayanin hanyoyin da suka gada ne waɗanda har yanzu ana amfani da tsarin duk da kasancewar akwai zaunannar hukuma a gwamnatance. Fasalin jagorori ana yi masu suna da masu riƙe da muƙamai ko Sarautun gargajiya. Hakan ya nuna cewa tsari ne bisa al'ada na jagorantar al'umma wanda aka gada iyaye da kakanni.



## 4.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- Abin da ake nufi da shugabanci
- Sanin aikin kowane Shugaba
- Iya gane matsayin Shugaba cikin rukunin masu jagoranci na gargajiya.

## 4.3 Shugabanci

### 4.3.1 Maigida

Gida wurin ne inda ake samun maigidanci da iyalansa, wato mata ko matansa da ‘ya’ya. Shugabanci ya fara ne daga cikin gida inda magidanci ke jagorancin duk wani da ke wannan gida domin a ƙarƙashin kulawarsa suke. Hausawa sun tashi da al’adar cewa hakkin mai gida ne ya kula da ci da sha da lafiyar mata da ‘ya’yansa da duk wasu buƙatoci na rayuwa nasu.

### 4.3.2 Mai Unguwa

A lokacin da aka sami rukunin gidaje da suka taru suka zama unguwa guda, akan naɗa Mai unguwa. Mai unguwa shi ne zai jagoranci waɗannan mutane na unguwarsa. Duk wani rikici da ya shiga tsakanin maƙwabci da maɗwabci, alhakinsa ne ya ga an sasanta. Mai unguwa yakan sasanta rashin fahimta da ta samu tsakanin mata da miji. Haƙƙinsa ne ya kula da tsaron mutanen wannan unguwa. Tsarin jagoranci na masu Mai unguwa a ƙasar Hausa daɗaɗɗa ne wadda har yanzu tana da tasiri wurin jagoranci. Mai unguwa yana ƙarƙashin ikon Dagaci ne.

### 4.3.3 Dagaci

Shugaban da ke riƙe da ragamar jagorancin wani gari ƙarami shi ake kira da suna Dagaci. Akwai masu unguwanni da dama waɗanda ake samu ƙarƙashin Dagaci. Su ke kula da al’amuran da suka shafi unguwannin da suka samar da wannan gari da Dagaci ke jagoranta. Aikin dagaci ne ya kula da dukkan tsaro, da lafiya, da duniyar mutanensa, da taimakon masu unguwanni. Duk wani saƙo na doka ko wayar da kai, ko aikin gayya da za a yi domin raya gari, Dagaci yakan nemi masu unguwanni ne domin ya sanar da su, su kuma su isar da saƙon zuwa ga jama’arsu. Wannan tsari gadajje ne a wurin Hausawa ta ɓangaren shugabancin. Ana bayar da shugabanci na Dagaci ga wanda mahaifinsa ko kakansa ya taɓa yi. Hakan ya tabbatar da cewa abu ne da ya shafi hanyar rayuwar Hausawa da suka gada tun da daɗewa. Har yanzu akwai Dagatai a garuruwan ƙasar Hausa a matsayin jagororin al’umma.

### 4.3.4 Hakimi

Hakimi jagora ne cikin al’ummar Hausawa da ke jagorancin garuruwan Dagatai kimanin biyar zuwa goma. ƙarƙashin ikon kowane hakimi, ana samun garuruwa waɗanda Dagatai ke mulki. Dagatai suna ƙarƙashin

ikon Hakimi ne. Wannan tsari shi ma yana cikin shugabancin gargajiya na Hausawa. Sarki ne ke da alhakin naɗa sarautar Hakimi.

### 4.3.5 Sarki

Sarki shi ne shugaban da ya fi dukkan wani mai riƙe da sarautar gargajiya a faɗin ƙasar da yake kusan kowace ƙasa ko yanki na Hausawa suna da Sarakuna. Tsari ne na shugabanci wanda yake na gargajiya da ake gado wurin iyaye da kakanni tun lokaci mai daɗewa. Sarki yana da masu taimaka masa wurin gudanar da sha'anin mulki. Akwai masu sarautu na muƙamai a fada, da hakimai ƙarƙashin kowane sarki. Tun kafin zuwan Larabawa da Turawa, akwai Sarakuna a ƙasar Hausa. Kowane Sarki yana da ƙasa mai faɗing gaske. Misali, Sarkin Kano, da Sarkin Katsina, da Sarkin Daura, da Sarkin Zazzau, duk sanannun Sarakuna ne na Hausawa.

Auna Fahimta

4. Mece ce bautar gargajiya?
5. Yaya wuraren bautar gargajiya suke?
6. Waɗanne dalilai ke sa al'adar bangaskiya ta sauya daga gargajiya zuwa zamani?



### 4.4 Taƙaitawa

A taƙaice wannan darasi ya bibiyi yadda shugancin Hausawa yake tun daga kan maigida zuwa Sarki. An fahimci cewa shugabanci yana farawa ne daga kan mai gida a mafi ƙaranci; babba fiye da kowane shugaba a al'adar Hausawa shi ne Sarki. Ganin cewa tsari ne da aka gada, akan kira su da Sarakunan gargajiya, wato hanyar jagorantar al'umma wadda aka gada wurin iyaye da kakanni.

### 4.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi

Hakimi: - jagora ne cikin al'ummar Hausawa da ke jagorancin gararuwan Dagatai kimanin biyar zuwa goma.

## 4.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari


Adamu, M. (1979). The Spread of Hausa Culture In West Afrika. In *Savanna Jounal of the Environmental and Social Sciences*. Zaria: Ahmadu Bello University press Ltd.

Auta, A. L. (2006). Tattalin Arziƙin Al'umma: Nazarin Sana'o'i Da Kasuwancin

Hausawa. A Cikin *Algaita Journal Of Current Research In Hausa studies Vol . 1 No: 4.* September. Kano: Bayero University.

Bargery, G. P. (1934). A Hausa–English Dictinary. London: Oxford University press.

Bunza, A. M. (2006). Gadon Feɗe Al'ada. Lagos: Tiwal Nigeria Limited.

Ɗangambo, A. (1987). Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa. Kano: Triumph.

Funtua, A. I. da Gusau, S. M. (ed) (2010). Al'adu da Dabi'un Hausawa da Fulani.
Kaduna: El-Abbas printers & Media Concept.

Greenber, J. (1947). *The Influence of Isam on a Sudaness Religion. Monograph of the American Ethnological society.* New York: J.J Augustin publishers.

Gusau, S. M. (2008). Waƙar Baka a ƙasar Hausawa: Yanaye-Yanayensu da Sigoginsu.
Kano: Bench Mark Pulishers

Ibrahim, M. S. (1982). Dangantakar Al'ada da Addini: Tasirin Musulunci a Rayuwar

Hausawa ta Gargajiya Kundin Digiri na Biyu, sashen Harsunan Nigeria. Kano: Jami'ar Bayero.

Nuhu, A. Tattalin Arziki Maguzawa a Rigar Zamani. Ph.D. Seminar. Department of Nigerian Languages, Sokoto: Usmanu [anfodiyo University

Sa'id, B. da wasu (ed) (2006). Ƙamusun Hausa na Jami'ar Bayero. Zaria: Ahmadu Bello University press Ltd.

Yahaya, I. Y. 1988. *Hausa a Rubucea. Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa*. Zaria:
Northern Nigerian Publication campany Limited.



**4.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta**

1- Mece ce dangantakar Sarki da sauran rukunan shuwagabanni?

Sarki shi ne shugaban da ya fi dukkan wani mai riƙe da sarautar gargajiya a faɗin ƙasar da yake kusan kowace ƙasa ko yanki na Hausawa suna da Sarakuna. Tsari ne na shugabanci wanda yake na gargajiya da ake gado wurin iyaye da kakanni tun lokaci mai daɗewa. Sarki yana da masu taimaka masa wurin gudanar da sha'anin mulki. Akwai masu sarautu na muƙamai a fada, da hakimai ƙarƙashin kowane sarki. Tun kafin zuwan Larabawa da Turawa, akwai Sarakuna a ƙasar Hausa. Kowane Sarki yana da ƙasa mai faɗing gaske. Misali, Sarkin Kano, da Sarkin Katsina, da Sarkin Daura, da Sarkin Zazzau, duk sanannun Sarakuna ne na Hausawa.

**RUKUNI NA UKU RABE-RABEN AL'ADA A IDON HAUSAWA**

Kashi Na 1 Al'adun Gargajiya Zalla.
Kashi Na 2 Al'adun Fasahar Hannu (Material Culture)
Kasha Na 3 Al'adun Fasahar Baka
Kashi Na 4 Cuɗaɗɗun Al'adu

**KASHI NA ƊAYA AL'ADUN GARGAJIYA ZALLA.**

**Abubuwan da Suke Ciki**

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufofin Darasi
1.3 Al'adun Matakan Rayuwa.
1.4 Camfe-Camfe
1.5 Iskoki
1.6 Maita
Auna Fahimta
1.8 Taƙaitawa
1.9 Ma'anar Muhimman Kalmomi
1.10 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
1.11 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



## 1.1 Gabatarwa

Gargajiya kalma ce da take wakiltar al'adar Hausawa. Haka kuma tana nufin tsafe-tsafe da camfe-camfe ko yanayin rayuwar da Hausawa suka gada wurin iyaye da kakanni. Al'adun gargajiya zalla suna bayani ne kan tsarin rayuwa wadda take da cikakken tasiri na Maguzanci musamman lamarin Iskoki. Darasin zai yi ƙoƙarin duban wasu daga al'adu waɗanda zallarsu grgajiya ce.



## 1.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- Abin da ake kira gargajiya.
- Waɗanne al'adu ne na gargajiya
- Bambancewa tsakanin al'adun gargajiya da na zamani.

## 1.3 Al'adun Matakan Rayuwa

Matakan rayuwa su ne aure da haihuwa da mutuwa. Waɗannan matakai cike suke da al'adu da ake gudanarwa a duk lokacin da aka zo yin su. Al'adar Hausawa ta gargajiya wadda ake yi lokacin aure ita ce 'Tsarince' inda saurayi zai je gidan su budurwa zance. Idan dare ya yi, nan za su kwana a ɗaki guda kan shimfiɗa ba tare da wani abu ya shiga tsakaninsu ba. Wata al'adar da ta danganci aure ita ce yin amfani da lafuzzan ashariya ko zagi a yayin ɗaurin aure. Irin wannan al'ada, sai dai gargajiya saboda yanayin nata na da ne.

A wurin haihuwa, tun lokacin da aka sami juna biyu ake ba mace mai juna biyu wasu magunguna na gargajiya waɗanda aka gada a gida. Haka kuma, mai juna biyu ba za ta riƙa fita waje ba idan dare ya yi, saboda gudun ka da Iskoki su haifar mata da matsala ga lafiyar junan biyun da take ɗauke da shi. Sunayen da ake sanya wa abin da aka haifa yana kasancewa na gargajiya ne wanda ya yi daidai da lokaci ko yanayi ko halin gida ko sitar jiriri ko abin da ya faru a lokacin da aka haifi jiriri. Misali, Tarana, ko Korau ko Hantsi ko Marka ko Nasare, da dai sauransu.

|angaren mutuwa akwai al'adu na gargajiya da ake yi da zarar an mutu. Misali, yanka ɗan akuya a matsayin al'ada a gasa a ci a daren ranar da wani ya rasu musamman namiji. Ana kiran wannan al'ada da suna 'biye gawa', a cewar Abdullahi (2008). Ana yin gumba a dafa giya bayan wasu kwanaki da mutuwa. Akan yi wa namiji buki na juya kafaɗa (Hawan Sadaka) aƙalla bayan shekara guda da mutuwa. Ire-iren waɗannan al'adun sun nuna cewa al'adun na gargajiya ne zallansu ba tare da ɓurɓushin wata al'ada daga wasu da ba Hausawa ba.

### 1.3.1 Camfe-Camfe

Ibrahim (1982) da Bunza (2006) sun ce camfi wasu aƙidoji ne waɗanda suke a zukatan Hausawa bisa yarda cewa in aka aikata wani abu, za a ga wani abu a matsayin sakamako. Irin wannan hanyar rayuwa ta Hausawa ta ƙunshi hani da horo. Misali,

a. Ba a fita ɗaki da dare sai an yi tari sau uku
b. Cin Aya yana ƙara ƙarfin gani
c. Idan mace ta ƙetare wanda, za ta yi mafarki
d. Yawan cin tuwon dawa yana ƙara ƙarfin gaɓoɓi.

### 1.3.2 Iskoki

Sa'id da wasu (2006:208) sun yi bayanin Iskoki da cewa mutanen ɓoye, watau aljanu. Shi kuwa Bunza (2006:1) cewa ya yi Iskoki a wajen Bahaushe wasu halittu ne masu kama da mutane ta fuskar halittarsu, da

suransu, da ayyukansu, da al'adunsu, da ɗabi'unsu, da harshensu, da siyasar rayuwarsu da dai makamantansu. Ke nan Iskoki wasu halittu ne masu kama da mutane waɗanda ba a gani. Ayyukansu sun bambanta da na mutane ta fuskar sauri da illata rayuwa ko yin abin ban mamaki ga wand aba Iska ba. Iskoki iri biyu ne akwai farare waɗanda ake mu'amala ta arziƙi da su. Baƙaƙen Iskoki su ne masu wuyar sha'ani saboda suna cutarwa da naƙasa rayuwa.

Al'adar Hausawa ta yarda akwai Iskoki, kuma suna tare da mutane a wurraren da suke. Hausawa suna ganin akwai wasu cututtuka da suke ganin Iska ce musabbabin samuwarsu ga jikin ɗan Adam. Misali, ciwon ɗankakkare, da ciwon mantuwa, da rashin haihuwa, da dai sauransu. Ana amfani da Iskoki domin su taimaka wurin samun abin duniya a sana'o'in Hausawa irin su noma da ƙira da Su.

### 1.3.3 Maita

Bunza (2006: 103) ya ce maita ɗabi'a ce ko aiki, sunan mai aikata ɗabi'ar ko aikin maye, a matsayin lito, mayu a matsayin jam'i. Ya kara da cewa ɗabi'a ce da mutum ke sayowa da kansa don ya hallaka ɗan'uwansa da sunan kare kansa daga wulaƙanci. To sai dai ana gadon maita wurin iyaye idan an sha a nono, ba sai an sayo ba. Duk maye, ya san cewa yana da wannan ɗabi'a. Bisa al'adar Hausawa, sun yarda cewa akwai maye. Yana kama kurwa ya cinye a mutu. In kuma an yi sa'a ta kuɓuta a rayu, ko idan an gane shi ne ya yi kamun a sanya ya saki wanda ya kama dolensa.

Bunza ya yi bayanin maye yana da sifofi uku da ake iya gane shi. Sifofin su ne bayyanannu, da ɓoyayyu, da jarrababbu. Wato ya kasance akwai wata fitacciyar alamar wadda bisa tsarin rayuwar Hausawa masu ita mayu ne, ko kuma ya kasance sifar maitar a ɓoye take. In kuma ba haka ba, mayen ya faɗi da kansa ko ya bayyana ƙiri-ƙiri gaban mutane su shaida. Waɗannan wasu ke nan daga cikin al'adun Hausawa waɗanda gargajiya ce zalla. Abin da ya sanya su zama gargajiya zalla yana da nasaba da tasirin ban gaskiya da hidimar Iskoki dangane da faruwar wasu abubuwan a wurin yadda suke faruwa.

Auna Fahimta

| | |
|---|---|
| 1- | Mene ne Maita? |
| 2- | Kawo camfi guda biyar |



## 1.4 Taƙaitawa

Ban gaskiyar Hausawa dangane da al'adun gargajiya suna da yawa. Misali, Dodo, da Fatalwa, da Kohi da Faɗe, da Kanbun Baka, duk suna cikin al'adun gargajiya zalla. An kawo camfi da Iskoki da maita ne a matsayin misali domin su wakilci sauran.

## 1.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi

Maita: - Ɗabi'a ce ko aiki

## 1.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari


Abdullahi, I. A. (2008) Jiya Ba Yau Ba: Waiwayen Al'adun Matakan Rayuwar

Maguzawa Na Aure da Haihuwa da Mutuwa. Kundin Digiri Na Uku, Sashen Harsunan Nigeriya. Sokoto: Jami'ar Usmanu [anfodiyo.

Adamu, M. (1979). The Spread of Hausa Culture In West Afrika. In *Savanna Jounal of the Environmental and Social Sciences*. Zaria: Ahmadu Bello University press Ltd.

Auta, A. L. (2006). Tattalin Arziƙin Al'umma: Nazarin Sana'o'i Da Kasuwancin

Hausawa. A Cikin *Algaita Journal Of Current Research In Hausa studies Vol . 1 No: 4.* September. Kano: Bayero University.

Bargery, G. P. (1934). A Hausa–English Dictinary. London: Oxford University press.

Bunza, A. M. (2006). Gadon Feɗe Al'ada. Lagos: Tiwal Nigeria Limited.

Ɗangambo, A. (1987). Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa. Kano: Triumph.

Funtua, A. I. da Gusau, S. M. (ed) (2010). Al'adu da Dabi'un Hausawa da Fulani.

Kaduna: El-Abbas printers & Media Concept.

Greenber, J. (1947). *The Influence of Isam on a Sudaness Religion. Monograph of the American Ethnological society.* New York: J.J Augustin publishers.

Gusau, S. M. (2008). Waƙar Baka a ƙasar Hausawa: Yanaye-Yanayensu da Sigoginsu.

Kano: Bench Mark Pulishers

Ibrahim, M. S. (1982). Dangantakar Al'ada da Addini: Tasirin Musulunci a Rayuwar

Hausawa ta Gargajiya Kundin Digiri na Biyu, sashen Harsunan Nigeria. Kano: Jami'ar Bayero.

Nuhu, A. Tattalin Arziki Maguzawa a Rigar Zamani. Ph.D. Seminar. Department of Nigerian Languages, Sokoto: Usmanu [anfodiyo University

Sa'id, B. da wasu (ed) (2006). Ƙamusun Hausa na Jami'ar Bayero. Zaria: Ahmadu Bello University press Ltd.

Yahaya, I. Y. 1988. *Hausa a Rubucea. Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa.* Zaria:

Northern Nigerian Publication campany Limited.

**1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta**

1- Mene ne Maita?

Maita ɗabi'a ce ko aiki, sunan mai aikata ɗabi'ar ko aikin maye, a matsayin lito, mayu a matsayin jam'i. Ya kara da cewa ɗabi'a ce da mutum ke sayowa da kansa don ya hallaka ɗan'uwansa da sunan kare kansa daga wulaƙanci. To sai dai ana gadon maita wurin iyaye idan an sha a nono, ba sai an sayo ba. Duk maye, ya san cewa yana da wannan ɗabi'a. Bisa al'adar Hausawa, sun yarda cewa akwai maye. Yana kama kurwa ya cinye a mutu. In kuma an yi sa'a ta kuɓuta a rayu, ko idan an gane shi ne ya yi kamun a sanya ya saki wanda ya kama dolensa.

2- Kawo camfi guda biyar Sunayen Ubangiji

i- Ba a fita ɗaki da dare sai an yi tari sau uku

ii- Cin Aya yana ƙara ƙarfin gani

iii- Idan mace ta ƙetare wanda, za ta yi mafarki

iv- Yawan cin tuwon dawa yana ƙara ƙarfin gaɓoɓi.

v- Ƙaton kai yana ƙarabasira

# KASHI NA BIYU AL'ADU FASAHAR HANUU

## Abubuwan da Suke Ciki

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufofin Darasi
2.3 Misalan Ire-Iren Fasahohin Hannu na Hausawa
  2.3.1 Ƙira
  2.3.2 Saƙa
  2.3.3 Dukanci
  2.3.4 Jima
  Auna Fahimta
2.4 Taƙaitawa
2.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi
2.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



## 2.1 Gabatarwa

Rabe-raben al'adun Hausawa ya nuna cewa akwai waɗanda suke a bayyane, ana iya ganinsu kamar yadda ake ganin masu aiwatar da su. Al'adun sun kasance fasahohin hannu da Hausawa kan gudanar domin samun kayayyakin aikin gida ko gini ko lufafi da dai sauransu.



## 2.2 Manufofin Darasi

i. A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci: Yin bayanin bayyanannar al'ada.
ii. Bayar da misalin bayyanannar al'ada da abin da ta ƙunsa.
iii. Iya bambance bayyanannar al'ada da sauran ɓangarorin rabe-rabe na al'adu.

.



## 2.3 Misalan Ire-Iren Fasahohin Hannu na Hausawa

Fasahohin hannu na Hausawa suna da yawa, kuma dukkansu bayyanannu ne a matsayin al'adunsu na gargajiya. Daga cikinsu ne za a yi bayani guda huɗu kamar haka:

### 2.3.1 ƙira

ƙira sana’a ce ta sarrafa ƙarfe domin a samar da kayan aikin noma ko farauta ko makaman faɗa ko wasu kayan amfani na gida. Maƙera iri biyu ne. Maƙeran Baƙi da Maƙeran fari. Maƙeran baƙi su ne masu ƙera fartanya da garma da sauran kayan aikin gida ko gona. Maƙeran fari su ne masu yin ƙere-ƙeren kayan ado irin su zobe, da sarƙa.

Wannan al’ada ta gado ce, uba yana koya wa ‘ya’yansa da zarar sun fara girma. A duk wurin da ake yin ƙira, galibi a ƙofar gida ko gefe can ake yin maƙera. Kayan aikinta da abin da ake ƙerawar a bayyane suke. Ana amfani da awartaki da kulfi da zarto da uwar maƙera da guduma da gawayi domin sarrafa ƙarfe. Hausawa sun gaji wannan al’ada a wurin iyaye da kakanni. Da wuya ka sami rukunin gidajen Maguzawan da ba su Maƙeri, saboda al’ada ce da suka gada iyaye da kakanni, a cewar Akodu (1985) da Nuhu (2020).

### 2.3.2 Saƙa

Sa’idu da wasu (2006: 384) sun ce, saƙa ita ce aikin sassarƙa zare da abawa don fitar da ƙyalle ko kuma sarrafa kaba don a yi tabarma ko faifai ko malafa ko mafici da sauransu. Wannan bayani ya nuna cewa saƙa iri biyu ce. Ta farko ita ce saƙar da ake yi da zare wanda aka samar daga audugar da aka kaɗa zuwa gwado. Ta biyu ita ce saƙar da ake yi da ganyen kaba a samar da tabarma ko mafici ko adudu da mangala da sauransu.

Ganin cewa akwai kayan da ake amfani da su kafin a samar da abin da aka saƙa, ya sa al’adar ta zama bayyananna. Saƙa a ƙasar Hausa tana tafiya ne da lokaci. da muhalli, wato sai wurin da ake samun auduga da kabar da ake yin kowace saƙar. Galibi ana yin saƙar da kaka bayan an kawar da amfanin gona.

### 2.3.3 Dukanci

Dukanci sana’a ce ta sarrafa jemammiyar fata domin yin jaka ko takalmi ko ɗinkin guru da laya da kambu. Bayyanannar sana’a ce ta gargajiya da ake aiwatarwa a ƙasar Hausa tun da daɗewa. Unguwannin da ake aiwatar da sana’ar a ƙasar Hausa akan kirasu da suna ‘Dukawa’, mai yin sana’ar ana kiransa ‘Baduku’. Sana’ar dukanci ta dogara ne da sana’ar jima wadda ta ƙunshi yadda ake fitar da gashi daga jikin fatar dabbobi, a gyara ta ta yi laushi da taushi.

### 2.3.4 Jima

Jima ita ce cire gashi daga jikin fatar dabbobi. Ana yin amfani da bagaruwa da katsi da baba da toka domin su zama sinadaran da za su taimaka gashin da ke jikin fata ya fita, sai a gyara ta yi taushi domin dukawa su ji daɗin sarrafawa zuwa wasu abubuwa na amfani ga jama'a. Ita ma wannan al'ada sana'a ce ta gado ga Hausawa. Ana yi mata kirari da ''Jima romon Jaɓa, ga kitse, ga wari'' wato aiki ne da yake da wuya kasancewar sai an tsuma fata ta jiƙa tana wari kafin a fitar da gashin da ke jikinta. To amma a ƙarshe in an gama jimar, ana samun alheri mai yawa mai daɗi bayan an sha wannan wari.

Auna Fahimta

| | |
|---|---|
| 1- | Me ake nufi da Saƙa? |
| 2- | Yi bayani kan sana'ar jima. |

## 2.4 Taƙaitawa

A taƙaice fasahar hannu su ne al'adun da Hausawa suka gada a matsayin hanyar gudanar da rayuwa da ke taimakawa wurin bunƙasa tattalin arziki. Al'adun su ne sana'o'i irin su ƙira saƙa da Su, da Fawa, da dukanci, da jima, da noma, da gini, da sauransu.

## 2.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi

Jima: - ita ce cire gashi daga jikin fatar dabbobi.

## 2.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

Abdullahi, I. A. (2008) Jiya Ba Yau Ba: Waiwayen Al'adun Matakan Rayuwar

Maguzawa Na Aure da Haihuwa da Mutuwa. Kundin Digiri Na Uku, Sashen Harsunan Nigeriya. Sokoto: Jami'ar Usmanu [anfodiyo.

Adamu, M. (1979). The Spread of Hausa Culture in West Afrika. In *Savanna Jounal of the Environmental and Social Sciences*. Zaria: Ahmadu Bello University press Ltd.

Akodu, A. (1985) A Comparative Study of the Traditional and Contemporary Arts of the Maguzawa of Kano and Kaduna states Ph.D. Thesis, Department of Fine Arts, Faculty of Enviroment Design. Zaria: Ahmadu Bello University.

Auta, A. L. (2006). Tattalin Arziƙin Al'umma: Nazarin Sana'o'i Da Kasuwancin

Hausawa. A Cikin *Algaita Journal Of Current Research In Hausa studies Vol. 1 No: 4.* September. Kano: Bayero University.

Bargery, G. P. (1934). A Hausa–English Dictinary. London: Oxford University press.

Bunza, A. M. (2006). Gadon Feɗe Al'ada. Lagos: Tiwal Nigeria Limited.

Ɗangambo, A. (1987). Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar

Hausawa. Kano: Triumph.

Funtua, A. I. da Gusau, S. M. (ed) (2010). Al'adu da Dabi'un Hausawa da Fulani.

Kaduna: El-Abbas printers & Media Concept.

Greenber, J. (1947). *The Influence of Isam on a Sudaness Religion. Monograph of the American Ethnological society.* New York: J.J Augustin publishers.

Gusau, S. M. (2008). Waƙar Baka a ƙasar Hausawa: Yanaye-Yanayensu da Sigoginsu.
Kano: Bench Mark Pulishers

Ibrahim, M. S. (1982). Dangantakar Al'ada da Addini: Tasirin Musulunci a Rayuwar

Hausawa ta Gargajiya Kundin Digiri na Biyu, sashen Harsunan Nigeria. Kano: Jami'ar Bayero.

Nuhu, A. Tattalin Arziki Maguzawa a Rigar Zamani. Ph.D. Seminar. Department of Nigerian Languages, Sokoto: Usmanu [anfodiyo University

Sa'id, B. da wasu (ed) (2006). Ƙamusun Hausa na Jami'ar Bayero. Zaria: Ahmadu Bello University press Ltd.

Yahaya, I. Y. 1988. *Hausa a Rubucea. Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa*. Zaria:
Northern Nigerian Publication campany Limited.

.

## 2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1- Me ake nufi da Saƙa?

Saƙa ita ce aikin sassarƙa zare da abawa don fitar da ƙyalle ko kuma sarrafa kaba don a yi tabarma ko faifai ko malafa ko mafici da sauransu. Wannan bayani ya nuna cewa saƙa iri biyu ce. Ta farko ita ce saƙar da ake yi da zare wanda aka samar daga audugar da aka kaɗa zuwa gwado. Ta biyu ita ce saƙar da ake yi da ganyen kaba a samar da tabarma ko mafici ko adudu da mangala da sauransu.

2- Yi bayani kan sana'ar jima.

Jima ita ce cire gashi daga jikin fatar dabbobi. Ana yin amfani da bagaruwa da katsi da baba da toka domin su zama sinadaran da za su taimaka gashin da ke jikin fata ya fita, sai a gyara ta yi taushi domin dukawa su ji daɗin sarrafawa zuwa wasu abubuwa na amfani ga jama'a. Ita ma wannan al'ada sana'a ce ta gado ga Hausawa. Ana yi mata kirari da ''Jima romon Jaɓa, ga kitse, ga wari'' wato aiki ne da yake da wuya kasancewar sai an tsuma fata ta jiƙa tana wari kafin a fitar da gashin da ke jikinta. To amma a ƙarshe in an gama jimar, ana samun alheri mai yawa mai daɗi bayan an sha wannan wari

## KASHI NA UKU AL'ADUN FASAHAR BAKA

### Abubuwan da Suke Ciki

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufofin Darasi
3.3 Ɓoyayyun Al'adun da ake ƙudurtawa a Zuci
3.4 Ɓoyayyun Al'adun da Aiwatarwa da Gaɓɓai Auna Fahimta
3.5 Taƙaitawa
3.6 Ma'anar Muhimman Kalmomi
3.7 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
3.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

### 3.1 Gabatarwa

Al'adun Fasahar Baka akasin al'adun gargajiya zalla da al'adun fasahar hannu ne, to sai dai suna da kusanci da ɗabi'a duk da yake ba ita ɗin ce ba. Abubuwan da mutum ya tashi ya ga ana yin su, kuma ya mayar da su a matsayin hanyar yin rayuwa wadda ya gada ko da kuwa ta wani aiki ko aƙida ce da ba a gani, ita ma ta zama al'ada ɓoyayya. Wannan fasali zai yi bayanin wasu al'adun fasahar baka da ake aiwatarwa da gaɓoɓi ko a ƙudurta a zuci su zama aƙida ko ta hanyar yin wani aiki.

### 3.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- Gane me ake kira da al'adun fasahar baka
- Sanin bambancin al'adun da suka shafi fasahar hannu da na fasahar baka.
- Bayar da misalan al'adun da suka ƙunshi fasahar baka iri daban-daban.

### 3.3 Ɓoyayyun Al'adun da ake ƙudurtawa a Zuci

Al'dun da suka kasance ɓoyayyu su ne abin da mutum ke ayyanawa a ransa su zama abin yi a rayuwa. Sukan kasance yadda ake tafiyar da rayuwa a tsakanin mai yin al'adar da wanda ake yi don shi. Galibi akan sami dalilin yin wannan al'ada ɓoyayya tsakanin wanda ke yi da wanda ake yi ta hanyar jin nauyi. Misali, kunya tsakanin Uwa da [a ko 'yar fari,

ko kuma kunyar da ke tsakanin suruki da surukai ko suruka da surukanta. A nan za a samu cewa aƙida ce ta kamun kai da jin kunya na rashin sakewa, da kasa aiwatar da wasu abubuwa idan ana tare da juna.

Baya ga kunya, alkunya tana cikin al'adun fasahar baka da ake aiwatarwa waɗanda suka zama cikin aƙidun Hausawa. Alkunya ita ce barin faɗi ko ambaton wani suna a dalilin kasancewar sunan na iyaye ko surukai ko 'ya'yan fari. A maimakon haka, idan za a kira sunan sai a yi ta kwatance ko inkiya domin nuna jin nauyin faɗin wannan suna.

Akwai kara wadda ita ma tana tafiya tare da kunya da alkunya. Kara ita ce nuna rangwame ko ragi tsakaninka da wani. Misali, idan abokinka yana kiran ƙanwar mahaifinsa da suna Gwaggo, to kai ma kana kiranta da sunan Gwaggo ya nuna ka yi masa kara. Haka kuma, idan wata hidima ta shafi aboki ko wanda ake tare, ka halarci taron ko yin wata ɗawainiya, wannan abokin ka yi wa kara. Irin waɗannan al'adu abubuwa ne da ake ƙudurtawa a zuci daga bisani su zama aƙidar tafiyar da rayuwa wadda aka saba yi tun da daɗewa har suka zama wani ɓangare na al'adu.

## 3.2 Ɓoyayyun Al'adun da Aiwatarwa da Gaɓɓai

Ana yin amfani da gaɓɓai domin yin wasu ayyuka da aka saba yi a rayuwa. Ta yiwu akwai wasu hanyoyi da ake iya bayyana abu, to amma sai aka zaɓi da a yi amfani da gaɓoɓi domin sauƙaƙawa ko sirrintawa. Wani lokaci kuma, al'adun fasahar baka hanyoyi ne da ke nuna halin da mutum yake ciki ko yin ishara ko isar da saƙo ga wani. Waɗannan al'adu su ne murmushi da dariya da yafuce da kyafce, da zumɓure da gunaguni da harara da ƙwata da tsaki da tagumi da daƙuwa da gwalo da gyatsine da murguɗe.

Galibin waɗannan misalai ana yin su ne domin a nuna halin da mutum yake ciki na jin daɗi ko rashinsa kamar kuka ko murmushi da dariya. Ana amfani da wasu a yi ishara da abokin magana kamar yafice da kaɗa hunne da murguɗe.

Wasu kuma ana amfani da su ne domin a nuna rashin jin daɗin abin da ya faru na mu'amala tsakanin mutum biyu ko fiye. Misali, zumɓure da tsaki da ƙwata.

Auna Fahimta

| 1- Mece ce ɓoyayyar al'ada? |
| --- |

## 3.4 Taƙaitawa

Wannan darasi ya dubi al'adun fasahar hannu ne a matsayin hanyar rayuwar Hausawa. Al'adu ne waɗanda ba a iya gani a taɓa, to amma ido na iya gani. Ganin da ido ke yi ba zai sa su zama bayyanannu ba, dalili shi ne wasu aƙidu ne, wasu ana amfani da gaɓoɓi. Al'adun su ne alkunya da kunya da kara da dariya da murmushi da ƙyafce da yafice da dai sauransu.

## 3.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi

## 3.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari


Abdullahi, I. A. (2008) Jiya Ba Yau Ba: Waiwayen Al'adun Matakan Rayuwar

Maguzawa Na Aure da Haihuwa da Mutuwa. Kundin Digiri Na Uku, Sashen Harsunan Nigeriya. Sokoto: Jami'ar Usmanu [anfodiyo.

Adamu, M. (1979). The Spread of Hausa Culture in West Afrika. In *Savanna Jounal of the Environmental and Social Sciences*. Zaria: Ahmadu Bello University press Ltd.

Akodu, A. (1985) A Comparative Study of the Traditional and Contemporary Arts of the Maguzawa of Kano and Kaduna states Ph.D. Thesis, Department of Fine Arts, Faculty of Enviroment Design. Zaria: Ahmadu Bello University.

Aminu, M. (1978). *Ma'anonin Tsabi'un Hausawa.* Kano: Aminu Zinariya Recording & Publishing Co.

Auta, A. L. (2006). Tattalin Arziƙin Al'umma: Nazarin Sana'o'i Da Kasuwancin

Hausawa. A Cikin *Algaita Journal of Current Research In Hausa studies Vol. 1 No: 4.* September. Kano: Bayero University.

Bargery, G. P. (1934). A Hausa–English Dictinary. London: Oxford University press.

Bunza, A. M. (2006). Gadon Feɗe Al'ada. Lagos: Tiwal Nigeria Limited.

Ɗangambo, A. (1987). Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa. Kano: Triumph.

Funtua, A. I. da Gusau, S. M. (ed) (2010). Al'adu da Dabi'un Hausawa da Fulani.
Kaduna: El-Abbas printers & Media Concept.

Greenber, J. (1947). *The Influence of Isam on a Sudaness Religion. Monograph of the American Ethnological society.* New York: J.J Augustin publishers.

Gusau, S. M. (2008). Waƙar Baka a ƙasar Hausawa: Yanaye-Yanayensu da Sigoginsu.
Kano: Bench Mark Pulishers

Ibrahim, M. S. (1982). Dangantakar Al'ada da Addini: Tasirin Musulunci a Rayuwar

Hausawa ta Gargajiya Kundin Digiri na Biyu, sashen Harsunan Nigeria. Kano: Jami'ar Bayero.

Nuhu, A. Tattalin Arziki Maguzawa a Rigar Zamani. Ph.D. Seminar. Department of Nigerian Languages, Sokoto: Usmanu [anfodiyo University

Sa'id, B. da wasu (ed) (2006). Ƙamusun Hausa na Jami'ar Bayero. Zaria: Ahmadu Bello University press Ltd.

Yahaya, I. Y. 1988. *Hausa a Rubucea. Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa.* Zaria:

Northern Nigerian Publication campany Limited.

## 3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

i- - Mece ce ɓoyayyar al'ada?

Ɓoyayyar al'ada ita ce wadda ta ƙunshi abin da mutum ke ayyanawa a ransa su zama abin yi a rayuwa. Sukan kasance yadda ake tafiyar da rayuwa a tsakanin mai yin al'adar da wanda ake yi don shi. Galibi akan sami dalilin yin wannan al'ada ɓoyayya tsakanin wanda ke yi da wanda ake yi ta hanyar jin nauyi. Misali, kunya tsakanin Uwa da [a ko 'yar fari, ko kuma kunyar da ke tsakanin suruki da surukai ko suruka da surukanta. A nan za a samu cewa aƙida ce ta kamun kai da jin kunya na rashin sakewa, da kasa aiwatar da wasu abubuwa idan ana tare da juna.

# KASHI NA HUƊU CUɗAɗɗUN AL'ADU

## Abubuwan da Suke Ciki

4.1 Gabatarwa
4.2 Manufofin Darasi
4.3 Cuɗaɗɗun Al'adu da Addini
4.4 Cuɗaɗɗun Al'adu da Zamani
Auna Fahimta
4.5 Taƙaitawa
4.6 Ma'anar Muhimman Kalmomi
4.7 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
4.8 Amsoshin Tambaypyin Auna Fahimta

## 4.1 Gabatarwa

aura daga wannan wuri zuwa wancan yana kawo sauyi cikin yanayin rayuwa. Haka kuma cuɗuwa da wata al'umma daban ko ɗaukar tsawon lokaci ko zuwan Larabawa da Turawa, sun sanya al'adun Hausawa sun cakuɗe. A irin haka, al'adun suna nan, to amma ba a sigar su ta asali ba. Wannan darasi zai waiwayi al'adun Hausawa musamman waɗanda suka cakuɗu da addini ko zamani.

## 4.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- Tantance ainihin al'adun asali na Hausawa.
- Bayyana cuɗaɗɗar al'ada.
- Fito da abin da ya cuɗu da al'adar Hausawa.

## 4.3 Cuɗaɗɗun Al'adu da Addini

Irin waɗannan al'adu za a ga cewa akwai tasirin addini a cikinsu. Misali, idan za a yi raɗin suna a yanzu, akan ce a karanta aya kaza, ko a yi salatin Annabi. A nan, an sami tasirin addini a kan wannan al'ada.

Nuhu (2020) ya yi bayanin wasu al'adu da ke cikin bukin mutuwar Maguzawa da ake kira juya kafaɗa ko bukin hawan sadaka. To sai ga shi ana gayyatar malamai domin su yi karatun Alƙur'ani a yayin bukin mutuwar Maguzawa. Wannan addinin Musulunci ne aka cakuɗa da al'adun gargajiya zalla.

Haka kuma a wurin binne gawar Maguzawa a yanzu, suna yin rami ne mai uwa da 'ya irin wanda Musulmi ke yi. Mamacin ana lulluɓe shi da farin yadi kwatankwacin yadda Musulmi ke yi. A nan ma an cakuɗa al'adar da addini. A lokutan bukukuwa ko idan za a sauya dabbar da iskar tsafin gida take kanta, wasu masu bin tsarin gargajiyar a yanzu suna neman Malamai su yi masu yanka na wannan dabbar, a cewar Nuhu (2020). Haka kuma irin wannan dabba akan yanka ta ranar juma'a. Nan ma, an cakuɗa wasu al'adun gargajiya da addinin Musulumci a ƙoƙarin samun yardar abokan hulɗa.

## 4.4 Cuɗaɗɗun Al'adu da Zamani

Bunza (2006: xxiv) ya ce: "Bayyanar Bature a ƙasar Hausa ya yi naso sosai a al'adun Hausawa musamman abubuwan da suka shafi aure, da haihuwa, da siyasa, da kasuwanci da zamantakewa". Al'adun da suka shiga irin wannan hali, sun zama cuɗaɗɗun al'adu da zamani. Idan ba a yi hattara ba, za su salwanta. To daman duk abin da ya cuɗu da baƙon abu, zai fara gurɓacewa a matakin farko kafin daga bisani ya salwance. Misali, zuwan Bature ya sa aka sami mota a matsayin abin sufuri maimakon jaki da doki. Idan mai mota zai wuce ka, sai dai ya yi maka oda a matsayin sallama ko ka gyara zai wuce. Wannan wata baƙuwar al'ada ce ta zamani.

Cuɗaɗɗun al'adu da addini ko zamani babu wurin da ba su kutsa ba cikin rayuwar Hausawa. Dalili shi ne, an samu cakuɗuwar Hausawa da ƙabilu na kusa da na nesa, ga zuwan saukakken addini, da ci gaban zama.

Auna Fahimta

| 1- An samu cakuɗuwar Hausawa da ƙabilu __________ |
|---|



## 4.5 Taƙaitawa

A taƙaice wannan darasi ya dubi yadda al'adun Hausawa suka cuɗe da addini, musamman na Musulunci da kuma zamani. Al'adun suna nan, to amma ana yin su haɗe da wasu baƙin al'adu.

## 4.6 Ma'anar Muhimman Kalmomi



## 4.7 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari


Abdullahi, I. A. (2008) Jiya Ba Yau Ba: Waiwayen Al'adun Matakan Rayuwar

Maguzawa Na Aure da Haihuwa da Mutuwa. Kundin Digiri Na Uku, Sashen Harsunan Nigeriya. Sokoto: Jami'ar Usmanu [anfodiyo.

Adamu, M. (1979). The Spread of Hausa Culture in West Afrika. In *Savanna Jounal of the Environmental and Social Sciences*. Zaria: Ahmadu Bello University press Ltd.

Akodu, A. (1985) A Comparative Study of the Traditional and Contemporary Arts of The Maguzawa of Kano and Kaduna states Ph.D. Thesis, Department of Fine Arts, Faculty of Enviroment Design. Zaria: Ahmadu Bello University.

Aminu, M. (1978). *Ma'anonin Tsabi'un Hausawa.* Kano: Aminu Zinariya Recording & Publishing Co.

Auta, A. L. (2006). Tattalin Arziƙin Al'umma: Nazarin Sana'o'i Da Kasuwancin

Hausawa. A Cikin *Algaita Journal Of Current Research In Hausa studies Vol. 1 No: 4.* September. Kano: Bayero University.

Bargery, G. P. (1934). A Hausa–English Dictinary. London: Oxford University press.

Bunza, A. M. (2006). Gadon Feɗe Al'ada. Lagos: Tiwal Nigeria Limited.

Ɗangambo, A. (1987). Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa. Kano: Triumph.

Funtua, A. I. da Gusau, S. M. (ed) (2010). Al'adu da Dabi'un Hausawa da Fulani.
Kaduna: El-Abbas printers & Media Concept.

Greenber, J. (1947). *The Influence of Isam on a Sudaness Religion. Monograph of the American Ethnological society.* New York: J.J Augustin publishers.

Gusau, S. M. (2008). Waƙar Baka a ƙasar Hausawa: Yanaye-Yanayensu da Sigoginsu.
Kano: Bench Mark Pulishers

Ibrahim, M. S. (1982). Dangantakar Al'ada da Addini: Tasirin Musulunci a Rayuwar Hausawa ta Gargajiya Kundin Digiri na Biyu, sashen Harsunan Nigeria. Kano: Jami'ar Bayero.

Nuhu, A. Tattalin Arziki Maguzawa a Rigar Zamani. Ph.D. Seminar. Department of Nigerian Languages, Sokoto: Usmanu [anfodiyo University

Sa'id, B. da wasu (ed) (2006). Ƙamusun Hausa na Jami'ar Bayero. Zaria: Ahmadu Bello University press Ltd.

Yahaya, I. Y. 1988. *Hausa a Rubucea. Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa.* Zaria:
Northern Nigerian Publication campany Limited

**4.8 Amsoshin Tambaypyin Auna Fahimta**

1- An samu cakuɗuwar Hausawa da ƙabilu __________ na kusa da na nesa

## KASHI NA BIYAR ƊABI'A

**Abubuwan da Suke Ciki**

5.1 Gabatarwa
5.2 Manufofin Darasi
5.3 Ma'anar [abi'a
 5.3.1 Bambancin Al'ada da [abi'a
 5.3.2 Kyawawan [abi'u
  5.3.2.1 Kawaici
  5.3.2.2 Gaskiya
  5.3.2.3 Riƙon Amana
  5.3.2.4 Kunya
 Auna Fahimta
5.4 Taƙaitawa
5.5 Ma'anar Wasu Kalmomi
5.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
5.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



### 5.1 Gabatarwa

Akwai kalmomi waɗanda ake yi masu musayar gurbi da wasu kalmomi a yayin ba su ma'anoni. A maimakon a ba su ma'anar da ta dace da su, sai a ɗauki ma'anar kalmar da ake ganin ko dai dukkan su abu guda ne, ko ake ganin suna da kusancin ma'ana. A wurin wasu Hausawa, suna kallon ɗabi'a ita ce al'ada. Duk abin da suke kira da suna ɗabi'a ko tsabi'a, to su a ganin su al'ada suke nufi. Ita kuwa ɗabi'a halaye ne na mutum shi kaɗai, ba a sauran al'umma ba. Wannan darasi zai mayar da hankali ne wurin duban ɗabi'a da bambancinta da al'ada.



### 5.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- Bambancin ɗabi'a da al'ada.
- Yadda ɗabi'a ke iya zama al'ada.
- Fayyace kyawawa da munanan ɗabi'a.

## 5.3 Ma'anar Ɗabi'a

Sa'id da wasu (2006:116) sun bayyana ɗabi'a da cewa ita ce halin mutum, ko al'adarsa wanda ke daidai da ɗabi'a. Gusau (2010: 3) cewa ya yi ɗabi'a halaye ne waɗanda mutane suke yi a ɗaiɗaikunsu kuma aka fahimci kowane mutum da irin hali nasa na daban da wani. Shi kuma Aminu (1978:1-2) cewa ya yi tsabi'a ita ce halin wani mutum da ya sha bamban da na sauran mutane. Kalmar ta fi shafar mutum guda, fiye da yadda ta shafi wasu rukunin mutane da yawa, balle kuma a danganta ta da harkokin rayuwar duniya gaba ɗaya. Waɗannan ma'anoni sun nuna cewa ɗabi'a halaye ne na ɗaiɗaikun mutane da suke yi waɗanda suka sha bamban da al'adun al'ummar da ya fito. Misali, a ce wane ya cika fushi kamar Soja, ko a ce wane yana da halaye irin na sarauta duk da ba ɗan sarauta ba.

### 5.3.1 Bambancin Al'ada da [abi'a

Akwai bambanci tsakanin al'ada da ɗabi'a, saboda kalmomin biyu suna da kusancin ma'ana ko ba su musayar ma'ana da wasu ke yi, ake tunanin abu guda ne. Al'ada hanya ce ta rayuwa wadda ta shafi dukkan al'umma. Al'ada ana gadonta ne wurin iyaye da kakanni. [abi'a kuwa hali ko halaye ne na mutum a karan kansa da yake yi shi kaɗai.

#### 5.3.1.1Kyawawan [abi'u

Daga cikin ɗabi'un Hausawa wanda ake samu a tsakanin ɗaiɗaikun mutane, akwai kyawawan ɗabi'un da aka iya samu da suka rikiɗe ya zuwa al'ada.

#### 5.3.1.2Kawaici

Sa'id da wasu (2006:24) sun bayyana kawaici da cewa Alkunya ko kau-da-kai ko haƙuri ko shiru-shiru. A faɗaɗe kawaici yana nufin kawar da kai daga wani hali da aka nuna ko aikata maka ba tare da ɗaukar mataki ba. Misali, idan Bahaushe yana bin ɗan'uwansa ko wani kuɗi, zai ɗauki lokaci ba tare da ya tambayi kuɗin ba. Haka kuma, idan wani yana yin rashin gaskiya ga abokin hulɗa, ɗaya zai yi shiru ne da sunan kawaici na tawon lokaci ba tare da ya nuna masa ba. Irin waɗannan halaye, ana samunsu cikin zamantakewar Hausawa.

#### 5.3.1.3 Gaskiya

Sa'id da wasu (2006:161) sun bayyana gaskiya da cewa nuna ko faɗar ko aikata abu a ainihin yadda yake. Abdullahi (2008) ya bayyana gaskiya a matsayin ɗaya daga cikin fitattun ɗabi'un Maguzawa da suka danganci al'adunsu. Ya nuna cewa duk wanda ya san Maguzawa, to zai

iya shaidar su da wannan ɗabi'a in dai ba sun sauya daga wannan halin ba. Ke nan, gaskiya a wannan bagire na rayuwar Maguzawa al'ada ce saboda hali na ƙwarai da ya shafi kowa a cikinsu. Wannan yana nuna yadda ɗabi'a ke juyawa ta zama al'ada a cikin al'umma. Zantukan hikimar Hausawa suna nuna hoton gaskiya a matsayin ɓangare na hanyar rayuwarsu. Misali,

Gaskiya Dokin ƙarfe
Gaskiya ɗaci gareta
Mai gaskiya ba ya shayi
Gaskiya ta yi halinta

**5.3.1.4 Riƙon Amana**

Amana ita ce ba mutum ajiyar kaya ko wani abu yadda zai adana shi kamar nasa ba tare da wani abu ya salwanta, ko wani abu ya sme shi ba, a cewar Sa'id da wasu (2006:15). Riƙon amana yana nufin mutum ya kasance mai hali na adana duk wani abu da aka ba shi ajiyarsa. Irin wannan hali ya zama jiki ga Hausawa. An shaide su da riƙon amana ta yadda har riƙon amana ta zama sashe na rayuwar da suka gada iyaye da kakanni.

**5.3.1.5 Kunya**

Kunya ita ce halin nuna kawaici da jin nauyi da rusunawa saboda wata dangantaka, a cewa Sa'id da wasu (2006:254). Kunya tana da kusancin ma'ana da kawaici. Dukkansu halaye ne na mutane a ɗaya-ɗayansu, na kawar da kai ga wani abu ta hanyar nuna jin nauyin magana kan wani abu. To sai dai a ɓangaren kunya, abin ya ƙunshi aikata wani abu ko ƙin aikatawa saboda jin nauyin dangantakarka da wani, ko gudun sakamako musamman mummuna. Kunya hali ne wanda ya rikiɗe ya zuwa al'ada saboda kasancewarta abin da aka tashi da shi wurin magabata. Kunya ta bayyana a zantukan Hausawa don tabbatar da cewa hanyar rayuwarsu ce. Ga wasu misali kamar haka: "Kunya adon gari".

Akwai irin waɗannan nagartattun halaye da Hausawa suke yi a rayuwa fiye da abin da aka yi bayani yanzu. An kawo misalai ne domin su wakilci sauran. Misali, akwai ladabi, da biyayya, da taimako, da kara da sauransu.

Auna Fahimta

| | |
|---|---|
| 1- | Zayyano kyawawan ɗabi'un Hausawa guda goma |

## 4.4 Taƙaitawa

Darasin ya yi bayanin ɗabi'a ne inda aka dubi alaƙar ɗabi'a da al'ada da abin da ya bambanta su. Har wa yau, an kawo bayanin wasu kyawawan ɗabi'u da suke rikiɗe zuwa al'adu kamar kawaici da gaskiya da riƙon amana da kunya. Muhimmancin amfani da alamomoin rubutun Hausa

## 4.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi

Kunya: - ita ce halin nuna kawaici da jin nauyi da rusunawa saboda wata dangantaka

## 5.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari


Abdullahi, I. A. (2008) Jiya Ba Yau Ba: Waiwayen Al'adun Matakan Rayuwar

Maguzawa Na Aure da Haihuwa da Mutuwa. Kundin Digiri Na Uku, Sashen Harsunan Nigeriya. Sokoto: Jami'ar Usmanu [anfodiyo.

Adamu, M. (1979). The Spread of Hausa Culture in West Afrika. In *Savanna Jounal of the Environmental and Social Sciences*. Zaria: Ahmadu Bello University press Ltd.

Akodu, A. (1985) A Comparative Study of the Traditional and Contemporary Arts of The Maguzawa of Kano and Kaduna states Ph.D. Thesis, Department of Fine Arts, Faculty of Enviroment Design. Zaria: Ahmadu Bello University.

Aminu, M. (1978). *Ma'anonin Tsabi'un Hausawa.* Kano: Aminu Zinariya Recording & Publishing Co.

Auta, A. L. (2006). Tattalin Arziƙin Al'umma: Nazarin Sana'o'i Da Kasuwancin

Hausawa. A Cikin *Algaita Journal Of Current Research In Hausa studies Vol . 1 No: 4.* September. Kano: Bayero University.

Bargery, G. P. (1934). A Hausa–English Dictinary. London: Oxford University press.

Bunza, A. M. (2006). Gadon Feɗe Al'ada. Lagos: Tiwal Nigeria Limited.

Ɗangambo, A. (1987). Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa. Kano: Triumph.

Funtua, A. I. da Gusau, S. M. (ed) (2010). Al'adu da Dabi'un Hausawa da Fulani.
Kaduna: El-Abbas printers & Media Concept.

Greenber, J. (1947). *The Influence of Isam on a Sudaness Religion. Monograph of the American Ethnological society.* New York: J.J Augustin publishers.

Gusau, S. M. (2008). Waƙar Baka a ƙasar Hausawa: Yanaye-Yanayensu da Sigoginsu.
Kano: Bench Mark Pulishers

Ibrahim, M. S. (1982). Dangantakar Al'ada da Addini: Tasirin Musulunci a Rayuwar

Hausawa ta Gargajiya Kundin Digiri na Biyu, sashen Harsunan Nigeria. Kano: Jami'ar Bayero.

Nuhu, A. Tattalin Arziki Maguzawa a Rigar Zamani. Ph.D. Seminar. Department of Nigerian Languages, Sokoto: Usmanu [anfodiyo University

Sa'id, B. da wasu (ed) (2006). Ƙamusun Hausa na Jami'ar Bayero. Zaria: Ahmadu Bello University press Ltd.

Yahaya, I. Y. 1988. *Hausa a Rubucea. Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa.* Zaria:
Northern Nigerian Publication campany Limited

**5.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta** Kawo ma'anar alamar rubutu

1- Zayyano kyawawan ɗabi'un Hausawa guda goma.

- i- Gaskiya
- ii- Riƙon amana
- iii- Kawaici
- iv- Zumunci
- v- Alƙawari
- vi- Kyauta
- vii- Yafiya
- viii- Tausayi
- ix- Girmamawa
- x- Kunya

## KASHI NA BIYAR MUNANAN [ABI'U

### Abubuwan da Suke Ciki

6.1 Gabatarwa
6.2 Manufofin Darasi
6.3 Munanan ɗabi'u
  6.3.1 Ƙarya
  6.3.2 Gulma
  6.3.3 Zamba
  6.3.4 Sata
  Auna Fahimta
6.4 Taƙaitawa
6.5 Ma'anar Wasu Kalmomi
6.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
6.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta



### 6.1 Gabatarwa

Idan aka samu abu mai amfani ko mai kyau, lallai ne ba ya rasa rashin amfani ko a ga wurin da yake da muni. Wannan tamkar gadajjen tsari ne cikin al'adu da ɗabi'un al'umma. [abi'un Hausawa ba su tsaya ga kyawawa kaɗai ba, akwai munana daga ɗaya ɓangaren. Munanan ɗabi'u su ma ana samun su ne a wurin ɗaiɗaikun mutane. Da wuya a samu mummunar ɗabi'ar da ta juya zuwa al'ada. Wannan darasi zai dubi wasu daga cikin munanan ɗabi'un Hausawa a matsayin wakilci na duk wata ɗabi'a maras kyau.



### 6.2 Manufofin Darasi

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- Bambancewa tsakanin mummunar ɗabi'a da kyakkyawa.
- Bayar da illar mummunar ɗabi'a ga mai yi.

### 6.3 Ma'anar Mummunar Ɗabi'a

Mummunan ɗabi'a ita ce halin mutum ko al'adarsa wanda ta saɓa da ɗabi'a na kirki.

Daga cikin ire-iren ɗabi' marasa kyau akwai sata da cin mutuncin mutane da kwace da zina da shaye-shaye da mudahana da sauransu**ƙarya**

Sa'id da wasu (2006:278) sun ce ƙarya ita ce maganar da ba ta gaskiya ba ce. Ƙarya ita ce faɗin magana musamman wadda abin da ba a yi ba, ko abin da ba haka yake ba. Irin wannan Magana ba al'ada ce ta kowa ba a al'ummar Hausawa, ɗabi'a ce ta ɗaiɗaikun mutane. ƙarya tana haifar da zubewar mutunci a idon al'umma don haka ne ma zantukan hikimar Hausawa suka nuna cewa ƙarya ba ta haifar da komi saboda ba ta yin dogon zango. Misali

ƙarya fure take, ba ta 'ya'ya
Ramin ƙarya kurarre ne.

### 6.3.1 Gulma

Gulma ita ce ɗaukar zance daga wani zuwa wani yadda zai kawo saɓani tsakaninsu, a cewar Sa'id da wasu (2006:173). Irin wannan hali ɗabi'a ce ta mutum guda; ba ta zama hanyar rayuwa ta al'adar Hausawa ba. A ƙarshe gulma tana haddasa faɗa tsakanin mutane. Su kuwa Hausawa suna da al'adar son zaman lafiya a cikin al'umma.

### 6.3.2 Zamba

Zamba ita ce ha'inta ko cuci ko yaudara, a cewar Sa'id da wasu (2006:489). Zamba galibi mai yin ta an yarda da shi ne a mu'amala, daga baya sai ya aikata zamba tsakaninsa da abokin hulɗa. Zambar na iya kasancewa aiki ne aka ba shi, ya yi ha'inci kansa, ko ya yaudari abokin hulɗa. Ita ma zamba ba ta cikin al'adun Hausawa da suka gada, to sai dai hali ne na ɗaiɗaiku a cikinsu. A lura cewa, irin wannan hali ana iya samunsa wurin wata al'ummar da ba Hausawa ba.

### 6.3.3 Sata

Sata ita ce ɗauke abin wani ba tare da sani ko yardarsa ba, a cewar Sa'id da wasu (2006:394). Wannan hali ana samunsa a cikin kowace irin al'umma. To sai dai babu wurin da ake samun sata a matsayin halin ƙwarai. Munin ɗabi'ar ya sa mai sata ba ya sakewa cikin jama'a, kowa yana gudunsa ko kaffa-kaffa da shi. Ko da ake samun masu satar hatsi cikin Maguzawa, ɗaiɗaikun cikin su ne ke yi waɗanda halinsu ya keɓanta da mafi yawansu. Nuhu (2020) ya bayyana cewa mai yuwuwa ne yana sace hatsi mutane, to amma ba ya mutuwa sai ya makance. Wanda ya saci kayan Bamagujen da yake yin tsafin Uwargona, zai tozarta ko ma ya kamu, ko ya mutu bayan kamuwa da rashin lafiya. Ke nan, tun a zama irin na Maguzanci, ɗabi'ar sata ta tsirarun mutane ce.

Haka kuma, sakamakon da ke biyo bayan yin sata mummuna ne ga mai yin ta.

Auna Fahimta

| | |
|---|---|
| 1- | Mene ne sata? |

## 6.4 Taƙaitawa

Ɗabi'un da aka ambata, ba su kaɗai ne munana ba. Akwai kwaɗayi, da munafunci, da tsegumi, da luwaɗi, da zunɗe, da keta, da sauran waɗanda aka yi bayani, misali ne aka kawo domin ganin irin halayen da ke iya bambanta da al'adun Hausawa.

## 6.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi

Zamba: - ita ce ha'inta ko cutar wani ko yaudara.
Sata: - ita ce ɗauke abin wani ba tare da sani ko yardarsa ba.

## 6.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari


Abdullahi, I. A. (2008) Jiya Ba Yau Ba: Waiwayen Al'adun Matakan Rayuwar

Maguzawa Na Aure da Haihuwa da Mutuwa. Kundin Digiri Na Uku, Sashen Harsunan Nigeriya. Sokoto: Jami'ar Usmanu [anfodiyo.

Adamu, M. (1979). The Spread of Hausa Culture in West Afrika. In *Savanna Jounal of the Environmental and Social Sciences*. Zaria: Ahmadu Bello University press Ltd.

Akodu, A. (1985) A Comparative Study of the Traditional and Contemporary Arts of the Maguzawa of Kano and Kaduna states Ph.D. Thesis, Department of Fine Arts, Faculty of Enviroment Design. Zaria: Ahmadu Bello University.

Aminu, M. (1978). *Ma'anonin Tsabi'un Hausawa.* Kano: Aminu Zinariya Recording & Publishing Co.

Auta, A. L. (2006). Tattalin Arziƙin Al'umma: Nazarin Sana'o'i Da Kasuwancin

Hausawa. A Cikin *Algaita Journal Of Current Research In Hausa studies Vol . 1 No: 4.* September. Kano: Bayero University.

Bargery, G. P. (1934). A Hausa–English Dictinary. London: Oxford University press.

Bunza, A. M. (2006). Gadon Feɗe Al'ada. Lagos: Tiwal Nigeria Limited.

Ɗangambo, A. (1987). Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar

Hausawa. Kano: Triumph.

Funtua, A. I. da Gusau, S. M. (ed) (2010). Al'adu da Dabi'un Hausawa da Fulani.

Kaduna: El-Abbas printers & Media Concept.

Greenber, J. (1947). *The Influence of Isam on a Sudaness Religion. Monograph of the American Ethnological society.* New York: J.J Augustin publishers.

Gusau, S. M. (2008). Waƙar Baka a ƙasar Hausawa: Yanaye-Yanayensu da Sigoginsu.
Kano: Bench Mark Pulishers

Ibrahim, M. S. (1982). Dangantakar Al'ada da Addini: Tasirin Musulunci a Rayuwar

Hausawa ta Gargajiya Kundin Digiri na Biyu, sashen Harsunan Nigeria. Kano: Jami'ar Bayero.

Nuhu, A. Tattalin Arziki Maguzawa a Rigar Zamani. Ph.D. Seminar. Department of Nigerian Languages, Sokoto: Usmanu [anfodiyo University

Sa'id, B. da wasu (ed) (2006). Ƙamusun Hausa na Jami'ar Bayero. Zaria: Ahmadu Bello University press Ltd.

Yahaya, I. Y. 1988. *Hausa a Rubucea. Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa.* Zaria:
Northern Nigerian Publication campany Limited

6.8 **Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta**

1- Mene ne sata?
Sata ita ce ɗauke abin wani ba tare da sani ko yardarsa ba,